# SHAIHU UMAR

**Na**

**Sir. Abubakar Tafawa Balewa**

*Shiryawa*

**Bukar Mada**

Shaihu Umar

ALLAH shi ne Sarki mafi ɗaukaka daga dukan Sarakuna, shi ne mafi tsarki daga dukan abubuwa, shi ne kuma Sarki wanda ba shi da makamanci. A kusa da Birnin Bauchi akwai wani ɗan gari ana kiransa Rauta. A cikin wannan ɗan gari, ya kasance akwai wani malami ma'abucin hankali, masanin taurari da Alƙur'ani da littattafai, kuma mariƙin addini. Shi malamin nan yana cikin mutane na duniya waɗanda Allah ya yi musu baiwa ta wajen fahintar abubuwa. Sunansa Shaihu Umar. Saboda tsananin saninsa da kuma hankalinsa, har labarinsa ya, isa ƙasashe masu nisa daga inda ya ke. Mutane suka yi ta fitowa daga ƙasashe, suna ta tahowa gare shi domin neman sani. Kafin a jima kaɗan sai ya zama mutane da su ke zuwa gare shi suka taru suka yi yawa, har suka rasa wajen yin gidaje, Saboda haka ya zama tilas ga waɗansu su nemi gidaje a cikin 'yan ƙananan ƙauyuka na kusa da Rauta.

Duk waɗanda su ke ɗaukar karatu a wajen Shaihu Umar ba su taɓa ganin wani tashin hankali game da shi ba, kuma ba su taɓa jin ranar da suka zo karatu ya ce musu ya gaji ba, sai ko in ba shi da lafiya. Ko rashin lafiya ne ya same shi, in ba mai tsanani ba, Ialle zai zo ya ba da karatu. Shi Shaihu Umar mutum ne wanda ya yi nisa, ba za a sami kamarsa ba. Kowane irin mugun abu ne ya same shi sai ya kan ce, “Allah shi ne mai sawwaƙewa." Bai taɓa fushi ba, kullum fuska tasa a sake ta ke, bai taɓa shiga magana wacce ba ta gamo da shi ba, ba ya gardama da kowa balle wata ‘yar tankiya ta tashi game da shi. Kai, don wannan hali nasa, har ya zama duk ƙasar babu wanda ya ke haye masa, kuma mutane da yawa sai suka fara cewa, “Lalle mutumin nan ba kawai ba, waliyi ne".

Wata rana wajen goshin la'asar bayan Shaihu Umar ya ba da karatu ga almajiransa, suna zaune suna taɗin duniya, sai wani almajirinsa ya tambaye shi cewa, “Ya mu'allim ni dai ina so in yi maka wata 'yar ƙaramar tambaya, amma ina shakka a raina kada ka yi zaton wai ko raini ne ya sa haka."

Shaihu Umar ya amsa masa, "Ai hankali bai taɓa cika ba sai game da tambaya, mutum kuma ba duka ya ke zamowa ya san kome ba. Saboda haka tambayi dukan abin da kake bukata, kada kuwa ka yi shakkar kome a cikin ranka. Ni kuwa Allah ya sa na san abin nan da za ka tambaye ni."

Matambayin nan ya ce, "Gafarta malam, abin da na ke buƙata in ji game da kai abu biyu ne. Na ɗaya dai, ka gaya mini inda ka fito, ka kuma bayyana mini Iabarin ƙasarku. Yadda ka ke ɗin nan duk mutanen ƙasarku haka su ke ? Don ni dai Lalle kana ba ni mamaki da yawa. Ba kuma ni kaɗai ba, dukan wanda ya san ka zai yi mamakinka. Na biyu, ina buƙata ka faɗa mini asalinka, domin na ga kai ba ka yi kama da mutanen ƙasarmu ba. Ga shi dai kana da sani da lafazi irin na Larabawa, amma na ga ba ka kai kanka can ba."

Umar ya amsa masa, "Haƙiƙa kuwa ka yi mini tambayoyi masu maʻana, waɗanda zan iya ba ka amsarsu ba da tantama ba. Kuma lalle ka tambayi labari mai tsawo, mai ban mamaki da tausayi ga dukan wanda ya ji. Yanzu zan yi ƙoƙari in ba ka labarin ƙasarmu da asalina, kuma da na yawace-yawace waɗanda na yi, da wahalar da na sha kafin in iso nan garinku."

Ni Mutumin Kagara Ne

DA can ni mutumin ƙasar nan ne, in ji Shaihu Umar, amma ko da ya ke haka ban girma na yi wayo a ƙasan nan ba. A can ƙasar Larabawa na girma. Ni dai tun fil azal mutumin wata ƙasa ce kusa da Bida. Sunan garimmu Kagara. Ubana kuwa wani mutum ne dogo, fari sana'arsa dukanci. Uwata mutumiyar Fatika ce. Yayin da a ke da cikina, ubana ya rasu, ya bar mini gadon shanu shida, da tumaki uku, da goɗiya tasa wacce ya ke hawa, sa'an nan kuma ita goɗiyan nan tana da ciki. Su waɗannan abubuwa duka sai aka danƙa su a hannun gyatumata, aka ce mata ta riƙe waɗannan sai sa'ad da Allah ya sa ta haihu, domin kayan ɗanta ne, kuma shi mijin nan nata ba shi da waɗansu dangi da za su ci gadonsa.

Ana nan ana nan, ran nan sai aka haife ni, na ksasance namiji. Da lokacin suna ya yi, sai uwata ta sa aka kama mata ɗaya daga cikin ragunan nan nawa, aka yanka, aka raɗa mini suna Umar. Muna nan dai, yayin da na zama ɗan shekara biyu, watau lokacin yaye, sai kakata ta wajen uba

ta karɓe ni domin ta yaye ni. Muka zauna tare da ita har ya zuwa lokacin da uwata ta yi buƙatan yin aure.

Sai uwata ta ce wa kakata, "To, kin ga ba ni da wani ɗanuwa a nan gari, daga ke sai wannan yaro, yanzu ina son aure, ga shi kuwa masu nemana da aure da yawa sun zaburo, sun ce lalle sai a ɗaura aure da wanda na fi so. Na kawo miki shawara, wane da wane su ne su ke nemana, amma fa har yanzu ban fid da gwani ba, ina so in ji abin da kika ce tukuna. A cikinsu kuwa akwai wani bafade na kusa da Sarki ainun wai shi Makau."

Da dai kakata ta ji sunan Makau a cikin maneman nan sai ta ce, "Ke, 'yan nan, ai Allah ya yi miki gyaɗar dogo ! Ga mai gani sarai, ki auri makaho? Ni dai in a shawarata ce babu wanda za ki aura sai Makau. Na san shi mutum ne mai kunya wanda ba shi da ƙaranta ko kaɗan. Shi kam lalle in kin aure shi gidanki lafiya".

Uwata sai ta yarda da wannan shawara, kashegari aka ɗaura aure, aka kuma ba da ranar da za ta tare. Da lokaci ya zo sai uwata ta tare ɗakinta, ni kuma ina tare da kakata. Muna cikin jin daɗin zama da kakata, sai ran nan ciwon ajali ya kama ta. Da dai ta ga ciwo babu dama sai ta aika aka kirawo gyatumata ta yi mata kashedi cewa, "Kin ga dai ban yi tsammani zan tashi daga wannan ciwo ba. Saboda haka ina so ki ɗauki wannan yaro, ki tafi da shi wurinki, domin ba ni son in gan shi yana kuka ko kaɗan, raina ya kan ɓaci da yawa a kan haka"

Gyatumata ta ce, "To".

Bayan ta fita kaɗan sai kakata ta cika, mutane suka taru da yawa, aka yi mata salla, aka kai ta kushewarta.

Bayan wannan ya ƙare, muna zaune cikin kyakkyawan hali tare da uwata a gidan Makau, sai ran nan Sarki ya sa aka yi kiran dukan fadawansa. Da suka taru ya ce musu, "Ba wani abu ne ya sa na kira ku ba, abin da na ke so game da ku shi ne ku yi shiri ku tafi ku yiwo mini hari a Kasar Gwari.

Ina da wata babbar buƙata ne, saboda haka ina son ku yi shiri maza ku tafi domin ku komo da hanzari".

Da fadawan nan suka ji wannan magana ta Sarki duka sai suka zama kamar mahaukata sabili da farin ciki, suka yi ta murna suna cewa, “Da ma mai neman kuka, balle an jefe shi da kashin awaki !" Dalilin farin cikinsu kuwa shi ne don ka sani a wajen harin nan za su yi samu da yawa na dabbobi har zuwa bayi. Kuma in sun dawo Sarki zai sam musu rubu'i daga cikin abin da suka samo. Ko wataƙila im mutum ya kama bayi uku  ne, sai Sarki ya ɗauki biyu daga ciki, shi kuma abar shi da ɗaya.

Wannan hari kuwa da Sarki ya shirya, dalilinsa wai don yana son ya sami waɗansu bayi ne waɗanda zai gama da nasa ya aika da su Kano, domin a sayo masa tufafi da kayan doki, waɗansu kuwa ya aika da su Bida domin a sayo masa bindigogi

A cikin baraden nan waɗanda Sarki ya zaɓa zuwa hari akwai Makau. Da lokacin tashinsu ya zo, bayan Sarki ya nema musu sa'a wurin wani malami sai Makau ya shigo cikin gida ya tara iyalinsa duka, ya ce musu, “To, yanzu kun ga zan tafi hari a Kasar Gwari ban san sa'ad da zan dawo ba. Ko a kashe ni a can Allahu a'alamu. Saboda haka ina so mu yi ban kwana, ku yafe ni abin da na yi muku duka, domin mutum na duniya duka in kana tare da shi, lalle wata rana za ka baƙanta masa zuciya"

Iyalinsa duka sai suka amsa gaba ɗaya suka ce, "Wallahi tallahi, mu dai babu abin da ka yi mana na ɓacin rai. Muna fata ka tafi lafiya, ka dawo lafiya." Dukammu muka fashe da kuka, babu mai jin na ɗan'uwansa.

Dukan masu zuwa harin nan suka yi ta shiri, asubar fari suka fita suka mika zuwa cikin Kasar Gwari. Suka yi ta tafiya har suka isa wani dan kauye na Arna a wata kwaifar dutse cikin kurmi. Da isarsu wurin duk suka sauka daga kan dawakansu, suka yi kwance a gindin itatuwa masu duhu, inda babu wanda zai iya ganinsu. A lokacin nan kuwa ruwan sama ya fara sauka, dukan manoma za su yi ta gyaran gonakinsu. Su kuwa arnan nan babu yadda za su yi su shuka wani amfani wanda zai ishe su ci har shekara, saboda haka sai su fito daga cikin garuruwansu, su sauko kasa

su shimfida gonaki a sarari. Amma duk da haka ba su da damar su yi aikin gonaki sosai ba saboda tsoron ‘yan hari.

Yayin da 'yan hari suka isa kauyen nan sai suka buya a bakin gonaki. Da sassafe wajen goshin asalatu, sai arna suka fara fitowa daga kauyukansu, suna zuwa gonakinsu. 'Yan hari kuwa suna kwance kurum, suna ganin dukan abin da su ke yi. Suka bari har dukan mutane suka fito. Bayan sun sake sosai suna ta aiki, suna tsammani babu wani abin da zai faru gare su, 'yan hari suka fada musu gaba daya, suka kama mata da maza har da kananan yara. Kafin arnan su ankara 'yan hari sun riga sun yi musu ta'adi. Nan da nan sai arnan suka fara fitowa da shirin yaki domin su kwaci 'yan'uwansu da aka kame. Af ! Kafin su shirya maharan sun yi nisa. Suka yi ta binsu, amma babu dama su same su, na gaba ya yi gaba, na baya sai labari.

## An Bata Tsakanin Sarki Da Makau

YAYIN da maharan suka ga sun kubuta, sai suka kama hanya sosai, domin an sani ba za su bi hanya ba don kada Arna su iske su. Da dai suka fada hanya sosai, sai suka yi ta hanzari, kowa yana ce wa dan'uwansa, "Sai ka zo." Suna ta tafiya har Allah ya sa suka iso gida lafiya. Da suka shigo cikin gari sai kowa ya kama hanyar zuwa fada, tare da abin da ya samo daga wajen hari. Dukansu daga mai bayi biyu sai mai uku har ma akwai mai hudu. Kowa daga cikinsu ya gabatar wa Sarki da abin da ya samu. Sai Makau kadai. Shi Makau da ya dawo bai bi ta fada ba, sai ya nufi gidansa. Amma wannan ba da nufin wani abu ba ne.

Da dukan mutane suka hallara, kowa ya ba da abin da ya kawo, sai Sarki ya ce, “Kai, ina Makau ? Ko an kashe shi ne a can ku ke boye mini?"

Jama'a duka suka amsa, “A’ a ! Ranka ya dade, ai ka san halin mntanen duniya. Mu da ma mun yi shiru ne kawai tun da farko da muka ga ka dauke shi, mu ga yadda za ku kare. Domin mun sani duk wanda aka ba shi amana ya ci lalle Allah yana kama shi, balle ma kamar kai da Makau wanda ya ke ka yarje masa kome naka. Bari dai mu fede maka biri har wutsiya, a cikin garin nan ba ka taba samun wanda ya ke cin amanarka kamarsa ba. Ai Makau ne ya ke fallasa ka a wajan talakawa da ka ke ganin suna girman kan nan yanzu. Kuma babu asirin da za ka yi da shi

wadansu ba su ji ba. Ka gani tun da muka fita zuwa harin nan har muka dawo bawan Allah nan bai bar zaginka ba, a kan haka ma har Sarkin Zagi ya yi hushi ya zare takobi zai yanke kansa, sai da barde ya ba shi hakuri. Yanzu ma abin da ya sa ba ka gan shi ba a nan, ya bi ta gidansa ne domin ya boye wadansu daga cikin bayin da ya samo, gama dai bawa hudu ya kama, mata biyu duka yara, da kuma yara maza biyu, amma dayan ya isa misali. Amma dai ba mu sani ba, ma ga abin da zai kawo."

Da Sarkin ya ji wadannan maganganu sai ya ce, "Daidai, amma Makau ya kyauta."

Bayan jimawa kadan, sai Makau ya tinkaro da 'yan bayinsa guda biyu wadanda ya kamo. Yana zuwa kawai da holokon ciki, bai san abin' da 'yan'uwansa fadawa suka kulla masa ba. Bayin nan kuwa da ya zo da su guda biyu su ne da ma abin da ya samu tun asali, cewa ya kamo bayi hudu karyar magabta ce. Da Makau ya kusanci kofar fada sai ya hango Sarki yana zaune a waje, ana ta fadanci. Da dai fadawa suka gan shi, sai suka fara cewa, “Ai ga Makau can yana zuwa da bayi biyu kawai, watau ya boye biyun ne ?" Da Makau ya iso wurin da Sarki ya ke ya fadi ya yi gaisuwa, amma Sarki bai amsa ba. Duk jama'ar wurin babu wanda ya ce masa ci kanka. Kowa dai sai kallonsa kawai ya ke yi, mahassadansa suna ta murna sai ka ce wadanda aka ba su gashin tozo.

Da aka jima kadan Sarki ya ce, "Makau, sai yanzu ka iso?"

Sai ya amsa ya ce, “A’a ranka ya dade, na bi ta gida ne domin in daure doki, in kuma sake shiga, sa'an nan in iso gare ka."

Sa'an nan Sarki ya ce, "To, bayi nawa ka samu ?"

Makau ya ce, “Biyu.”

Sarki ya ce, "Haka ne. Lalle ne bayi biyu ka samu kadai? Ka yarda in na yi bincike na iske ba bayi biyu ka samu ba, in yi maka abin da na so duka ?"

Makau ya ce, "Wallahi na yarda."

Da suka gama wannan magana, sai Sarki ya kira Sarkin Zagi, ya tambaye shi cewa, “Bayi nawa ne Makau ya samo daga wurin hari ?”

Sarkin Zagi da ma yana Allah Allah wannan abu ya auku. sai ya ce, "Bayi hudu, amma da biyu ya iso cikin garin nan domin ya sayad da biyun a hanya ga wani ayari na Kanawa wadanda za su tafi daukar daddawa a kasar Bauci. "

Sarki ya ce, “To, ka ji, Makau".

Shi kuma ya amsa, "Ranka ya dade, yanzu ni ai ba ni da ta cewa, domin wadannan mutane sun riga sun yamutsa magana, babu sauran abin da zan shaida maka ka yarda da shi."

An Washe Gidan Makau

Sai Sarki ya fusata, ya ta da fadawa ya ba su izni su je su washe gidan Makau, kada su bar masa kome ko da tabarma. Fadawan suka tafi, suka washe gidan kaf, hatta ciyawar da aka yi jinkar dakuna da ita sai da aka yaye. Kuma yana da wadansu 'yan shanu a wani dan kauye na kusa da gari, nan da nan sai aka sa wani ya je ya zo da su. Da aka tafi za a zo da shanun nan na Makau, sai aka hado da nawa wadanda ubana ya bar mini gado, duk da tumakina, da godiyata, da danta. Bayan an gama washe-washen nan duka, sai aka hada kayan aka kawo wurin Sarki.

Da aka kawo sai Makau ya tashi ya ce wa Sarki, “Ranka ya dade, ina rokon a cikin kayan nan, akwai wadansu wadanda su ke ba nawa ba, kamar godiyan nan da danta, da tumaki, da kuma

wadansu daga cikin shanun. Su wadannan na wani yaro ne maraya wanda na auro uwa tasa. Abin da na ke roko a fid da kayan marayan nan a mayar masa."

Da jin haka sai fadawa suka dauka gaba daya, "Mhm, kun ji ya fara irin karyan nan tasa ! Ina ka ga wata dukiyar maraya har daza ka ce tana wurinka? Allah ya dade da Sarki, karya ya ke yi. Ita dukiyar marayan da ya ke fadi ba wurinsa ta ke ba, tana wajen uwar yaro, ita ta san inda ta kai abinta." (A lokacin ina dan yaro karami babu wayo, balle in san abin da a ke yi. Ni dai kawai sa'ad da a ke washe gidammu, na ga iyayena suna kuka).

Nan da nan ba a yi ma ko da wani dam bincike ba, sai Sarki ya yarda da maganan nan da fadawansa suka gaya masa. Bayan wannan ta kare, sai ya ce wa Makau, "To, ka gani wannan shi ne sakamako wanda ka samu daga Allah, domin cin amanata da ka ke yi bayan na amince da kai. Kuma ni yanzu ba zan ce maka wani abu ba, abin nan da aka yi maka ma ya isa. Bayan wannan matukar ni na ke Sarki a wannan gari, ba zan yarda ka zauna a cikinsa ba. Saboda haka yanzu zan kore ka ka tafi can wani wuri inda ba hannuna. Kuma har yanzu ban hana ka tashi da iyalinka ba. Kowace mace cikin matanka in tana son ka sai ta bi ka ku tafi tare, in kuwa ba ta sonka, tilas ka bar ta."

Makau ya ce, "Ranka ya dade, na ji na karba. Amma ina roko a cikin darajar mulkinka ka bar ni in yi 'yan kwanaki kadan a nan domin in sami dan guzurin da zan ci a hanya, domin ka sani yanzu zan tafi wuri ne inda ban sani ba."

Sarki ya daga kansa zamani guda, kana ya amsa wa Makau cewa ya yarda, amma kwana hudu kawai ya ba shi ya shirya kaura tasa.

Makau ya yi godiya, ya taso ya zo gida, ya tara iyalinsa duka babba da yaro, maza da mata, ya ce da mu, "To kun gani yadda Allah ya kaddara wannan al'amari bisa gare ni. Sarki ya ce sai in bar masa kasarsa, amma ya yardam mini in tafi da mace wacce ta ke son ta bi ni, kuma bayan wannan ya ce kamin kwana hudu dole in bar garin nan. Yanzu abin da na ke so idan a cikinku akwai wacce ranta ya riya mata za ta iya daurewa ta bi ni, to".

Duk iyalina sai muka fashe da kuka gaba daya muna cewa, "Wallahi tallahi, ba wata kasa za ka tafi ba, ko da lahira in ana rakiya, lalle ba shakka ma raka ka."

Makau ya yi mana tambayoyi uku na shari'a, dukammu babu wanda bakinsa ya sake.

An Fitad Da Makau Daga Garin

BAYAN Makau ya aikata wannan abu wajen iyalinsa, sai ya fita zauren kofar gidansa ya zauna yana tunanin kasar da zai tafi, sai mutane da yawa sahibansa da makamantansu suka yi ta zuwa gare shi suna gaishe shi da wannan bakin ciki, yawancin mutanen in sun zo sai in ga suna kuka da hawaye, wadansu ku kuwa sai su zo da 'yan kudi su danka masa, suna cewa ga dan wannan ko ka sha ruwa a hanya.

Da almuru ta yi, sai Makau ya tashi ya yi alwala ya yi salla. Ran nan kuwa ran tuwon gyatumata ne. Bayan da aka gama hira duka sai Makau ya shiga gida domin ya kwanta. Da ya shiga sai ya wuce dakin uwata, ya same ta tana kuka babu yadda ta ke. Da ya ga haka sai ya ce mata, "Wannan abu ba na kuka ba ne, ya wuce kuka. Kuma ko ba haka ba, tun da ya ke Musulma ce ke, ya kamata ki tuna cewa dai dukan abubuwa daga Ubangiji su ke samun mutum saboda haka abin da ya fi kyau a garemu duka sai mu yi tawakkali ga Allah wanda ke aikata kome yadda ya so.”

Uwata ta amsa ta ce, “To, Makau yanzu ni kuwa a duniyan nan me zai hana mini kuka ? Ka ga dai dukan fadin garin nan ba ni da dangin uwa balle na uba, kuma ban da wannan dan maraya ba ni da kowa sai kai da Allah ya hada mu. Bayan wannan abin da na ke tunani yanzu shi ne wannan sharri da ya same ka. Domin lalle a duniyan nan abin da ya taba ranka nima ya taba nawa. Amma babban abin da na ke tunani shi ne wannan dan yaro, na rasa yadda zan yi da shi. Har yanzu kuma da ina da bukata in kun dawo daga wajen harin nan in tambaye ka izni in je garimmu in gano iyayena in dawo, to, ga abin da ya auku."

Da Makau ya ji wannan magana, sai ya yi kurum yana ta tunani. Bayan da aka jima sai ya amsa mata. “Hakika kina da abubuwa na bakin ciki tare da ke, amma ko da ya ke haka ne Allah mai sawwake kome ne. Share hawayenki babu kome cikin nufin Allah. Amma a kan zancen da kika ce na wajen zuwa duba iyayenki zan ba ki shawara guda. Yanzu tun da ya ke ya zama haka, ga kuma halin da mu ke ciki, ni kuwa ban san wani gari ba takamaimai inda zan zauna, saboda haka na yarje miki ki tafi ki duba gida, ni kuwa yayin da na sami wurin zama sosai zan aika miki ki same ni can. Yaron nan kuwa da ya ke ba za ki iya tafiya da shi ba, ya kamata ki bar shi a nan a wurin wani amintaccen mutum, har ki tafi ki dawo ki same shi."

Gyatumata ta ce, “To."

A kwana a tashi ran nan wa'adin da Sarki ya diba wa Makau na kwana hudu suka cika. Tun da sassafe Sarki ya aiko a gaya masa, yau fa alkawari ya cika, sai ya shirya ya yi dakon manzonsa wanda zai zo ya raka shi ya fitad da shi iyakar kasa. Tun kafin safiya ta yi Makau ya rigaya ya shirya sarai, amma manzon Sarki bai tashi zo masa ba sai bayan an yi sailar azahar. Makau yana zaune yana ta duban hanya, sai zuwa can ya ga Sarkin Zagi da wani wai shi Simili suna zuwa akan ingarmunsu. Da suka iso inda ya ke ba su ce masa kome ba, sai “Bismilla!"

Makau ya tashi, sai suka tambaye shi, “Wace jihar ka ke so mu fitad da kai ?"

Sai ya ce, “Ta wajen fuskar kasar zazzau.“

Suka ce, “Wuce mu tafi."

Suka sa shi a gaba suna ta ingizarsa har suka taho da shi kan iyaka. A nan suka bar shi inda tun da Allah ya yi shi bai taba zuwa ba. Suka ce masa, “Yanzu kuma sai ka san inda za ka, mu dai nan Sarki ya umarce mu mu tsaya, nan kuwa za mu bar ka, ko ka mutu, ko 'yan hari su same ka su kama babu abin da ya miskile mu."

Makau ya ce, "Haka ne, in kun je ku yi mini godiya wurin Sarki, ku kuwa Allah ya fishe ku daji, amin."

Makau Ya Sadu Da Maharbi

Da suka bar shi sai ya nemi gindin wata babbar itaciya ya zauna yana ta tunani, yana kiran Ubangiji da Ma'aikansa, har kwadayinsa ya fita. Da ya ta da kai sai ya ga wani maharbi yana yawo, daga shi sai kwari da baka. La'asar kuwa ta yi, Makau a lokacin nan kishirwa kamar za ta kashe shi. Maharbin nan da ganinsa sai ya nufo inda ya ke, ya same shi ya gama kai da gwiwa. Da ya iso sai ya yi masa sallama, Makau ya ta da kai ya amsa masa.

Bayan da suka yi gaisuwa, sai maharbin ya ce wa Makau. "Kai kuwa, bawan Allah, daga ina ka fito ? Ina dalilin zuwanka wannan wuri a wannan lokaci ? Ko kuwa kun je hari ne, rana ta baci muku kuka fantsamu cikin daji ?"

Makau ya ce, "Ko daya. Yanzu abin da na ke so tukuna ka ba ni ruwa in sha, kana in hankalina ya komo na ba ka labarin zuwa na wannan bigire."

Sai maharbi ya bai wa Makau ruwa. Bayan da ya sha ya jima kadan har duk hankalinsa ya komo jikinsa, sai ya ce wa maharbi, "Alhamdu lilahi, na gode, Allah ya saka maka da alheri bisa kan wannan taimako da ka yi mini. Ka ji ka ji sanadin zuwana wannan wuri."

Da maharbin ya ji wannan labari, sai ya yi mamaki yana cewa, "Hakika yadda Allah ya kaddaro abu haka ya ke faruwa. Mai gaskiya kuma har abada bai taba tabewa ba,"

Makau ya ce, "Ina dalilin wannan magana taka ?"

Shi kuwa ya ce, “I, na gani ne da Allah ya sa ka gamu da wani ne daga cikin 'yan'uwana, ba ni ba, lalle da ka zama bawa tuni. Amma ka ga da ya ke a kan gaskiyarka ne wannan sharri ya same ka abin ya zo da sauki, Allah kuma ya dada sawwake shi, ya taimake mu bisa dukan abin da za mu aika, ya hawad da mu bisa kan abokan gabammu. To, yanzu kuma wane gari ka ke yi nufin ka tafi ?"

Makau ya ce, "Wai da ni bukatata ina so in tafi wani dan kauye ne wanda ya ke tsakanin Zazzau da Kano, in yi zamana. Amma kuma ina so kauyen nan da zan zauna ya zama kasar wurin tana da kyau wajen amfani. Domin bukatata yayin da na sami matsuguni sosai sana’ar da zan yi ita ce noma. Bayan na zauna kuma na dan gyara gida ina so in aika iyalina su zo."

Ka Zauna A Makarfi

Maharbi ya ce, “Kai ! Lalle wajen daukar sana'a ka yi babban zabi. Tun da ya ke haka ne zan ba ka wata ’yar shawara kadan in ka yarda, to, in kuma ba ka yarda ba, to. Shawaran nan ita ce a gaba da Zazzau a hanyar Kano, akwai wani dan gari sunansa Makarfi. Mutanen garin kuwa sanannu ne wajen aikin gonaki, noma a can yana da riba, amfaninsu kuwa kullum mai albarka ne. Ina tsammani ya fi kyau a gare ka ka tafi wurin ka zauna. Ka ga a can kuma babu wani wanda zai dame ka, duk mutanen garin babu wanda ya ke shiga cikin sha’anin dan’uwansa, domin kowa a cikinsu yana da gwargwadon samunsa. Ka kuwa sani tsegumi ba ya yin yawa a wurin da yalwa ta ke, sai dai wurin da fatara ta kafe gindinta.”

Makau ya sunkuyad da kansa ya dade, sa’an nan ya ta da kai ya ce, “Wallahi, ni yanzu abin da ka fada mini duka zan yarda, domin dai na ga babu shakka kana kaunata. Saura ina so in tambaye ka wani dan asiri wanda ya ke zan yi in kubuta daga hadari wanda zan hadu da shi kafin in kai Makarfi.”

Sai maharbin ya kawo wata 'yar laya mai sasari ya ba shi, ya ce masa “Wannan ita ce abar da na taimake ka da ita, kuma ina fata ka isa laflya. Allah ya kau da bacin rana." Suka yi ban kwana, sa’an nan suka rabu, ko wanne cikinsu yana kuka.

Makau Ya Tasam Ma Zazzau

SAI Makau ya tashi a tsaye bayan da suka yi ban kwana da maharbi, ya dan jima kadan a wurin da ya tsaya, domin bai san hanyar da zai bi ba ta zuwa Birnin Zazzau. Da maharbin ya ga haka sai ya komo ya kama hannunsa, suka yi ta tafiya har suka fada a wani labi kusa da wani dan kauye. Da suka tafi wurin sai maharbi ya ce masa, "Ka ga wannan dan kauye na gabam mun nan, ta nan za ka bi, amma kada ka yarda ka shiga cikin garin, domin kuwa watakila in ka shiga ba za ka kara fita ba har abada. Ya fi maka kyau ka raba ta gefen garin ka wuce. Kuma ka yi hankali lokacin da za ka wuce, kada ka bi ta baryar arewa, domin a arewa da garin akwai gonar wani mutum wanda ya ke mai sihiri da gaske. Ko wane mutum in dai bako ne, ko kuwa bawa wanda ya gudo daga wata kasa yayin da ya iso inda gonan nan ta ke, sai ya tsaya a wurin, ya rasa hanyar da zai bi, tilas sai ya shiga cikin gonar. Kullum kuwa shi mutumin nan bai taba rabuwa da gonarsa ba. Saboda haka in ya ga mutum ya tsaya kusa da gonar yana dawainiya sai ya zo ya kama shi ya maishe shi bawansa."

Makau ya ce, "To, na ji." Suka sake yin ban kwana a wurin, Makau ya yi gaba, maharbi ya koma da baya zuwa inda da ya hadu da Makau.

Makau ya kama hanya har dai ya iso inda garin nan ya ke. Da ya zo sai ya ki shiga ciki, ya yi aiki da dukan abin nan da maharbi ya gaya masa. Tun da ya kama hanya bai waiwaya ma ya dubi garin ba, sai da ya tabbata a ransa cewa ya ba shi baya da gaske. Yayin da ya ga ya tsere daga garin nan sai ya nemi gindin wata itaciya ya zauna ya huta, ya kuma ci dan abinci.

Bai jima da zama ba sai ya ji kofatan dawaki a dama da shi, kuma ya ji maganar mutane kowa yana ba dan'uwansa labarin abin da ya yi yayin da suka tafi hari a wadansu wurare. Da jin haka, sai Makau ya hau bishiyar da ya ke gindinta, ya buya a cikin rassanta.

Da suka iso wurin sai wani daga cikinsu ya ce, "Kun ga a wannan wuri mun taba yin fada da wane da wane yayin da mu ke dawowa daga hari. Ran nan ba mu sami kome ba sai wani dan yaro karami wanda shekarunsa ba su wuce bakwai ba. Mu kuwa mu uku ne.

“Da muka iso nan muka tsaya muna hutu, sai wani daga cikimmu ya ce, “To, yanzu ina dabarar da za mu yi da yaron nan ? Yaya kowane dayammu zai sami ladar wahala tasa daga gare shi ?"

“Da jin wannan jawabi sai wanda yaron nan ke wurinsa ya yi farat ya ce, “Wane, me ka ke nufi da fadin wannan magana mara dadi haka? Ashe kai dai kaza ne. Yaya za ka ce wai kana son wata moriya a jikin wannan yaro, bayan ni na sha wahala, ni daya na kama shi. In da dadi me ya hana ka kamo naka ?"

“ Dayan kuwa da jin wannan magana, nan da nan ya zaro takobinsa, ya ce, “To, yanzu zan tabbata maka cewa wannan yaro ba naka ne kai daya ba.

“ Da ya cira takobin bai fasa ba sai ya fille kan yaron, yace da maigidansa, “To, ka ce kai ka kamo shi, dauki gangar jikin Iadan wahalarka, mu biyu kuwa kan ya ishe mu.

“Bayan da mutanen nan suka gama tadi suka huta, sai suka tashi, kowa ya dare bisa kan dokinsa. Suka kama hanya sosai da hanzari. Da Makau ya ga sun yi nisa sai ya sauko. Yayin da ya ke saukowa sai ya ga wani abu a gindin itaciya, ashe jaka ce daya daga cikin mutanen ya yar, babu kome cikinta sai liyarai. Sai ya dauka, ya kama hanya yana take da sawunsu har kwana guda, ba hutu balle ya tsaya ya ci abinci.

Ya Ga Ganuwar Birni.

Yana cikin tafiya sai ya hango ganuwar gari dam gabansa. A lokacin nan kuwa masu dawakin sun rigaya sun shiga cikin gari. Makau ya yi ta tafiya har ya iso kofar garin ya shiga. Ya ce wa Sarkin Kofa, “Malam, wane gari ne wannan ?"

Sarkin kofa ya ce, “Birnin Zazzau ke nan, abokina."

Da jin haka Makau ya ajiye zuciya, ya ce, “Alhamdu lillahi Allah kai ne mai arzutawa !"

A nan bai gusa ba suka yi abota da Sarkin Kofa, har Sarkin Kofa ya ce, “Raina ya yi fari da ganinka, lalle sai ka bakunce ni."

Makau ya yi murna, ya sauka gidan Sarkin Kofa. Da dare ya yi suka ci abinci. Bayan da suka gama suka wanke hannayensu, suka shiga tade-taden duniya. Makau kuwa ya habarta wa Sarkin Kofa dukan abin da ya same shi.

Sarkin Kofa ya tambaye shi, “Yanzu ina ka ke nufin tafiya ?"

Makau ya ce, “Na ji labarin wani kauye ne a kasan nan sunansa Makarfi, ina so in tafi can in duba ko na iya zama, don na ji kasar tana da kyau ga noma."

Sarkin Kofa ya ce, “To, madalla, ni ma ina da wani shakikina a can sunansa Tanimu, in za ka tashi sai in ba ka takarda zuwa gare shi."

Da gari ya waye, Makau ya nufi wurin Sarkin Kofa ya ce zai tashi amma yana so ya hada shi da wani yaro su tafi kasuwa ya sayi wadansu kaya. Sarkin Kofa ya hada shi da yaronsa, suka tafi. Makau ya sayi fartanya da gatari da masassabi da sungumi. Da ya gama saye-sayensa ya komo gida. Suka yi sallama da Sarkin Kofa, ya kawo guzuri ya ba shi. Ya rubuta takarda zuwa ga dan'uwansa Tanimu, ya ce:

“Bayan gaisuwa, ga wannan mutum sunanasa Makau, mutumin kirki ne, na turo shi gare ka. Sai ka tambaye shi labarinsa, da kuma dalilin da ya sa ya fito daga garinsu. Kuma ya ce yana so ya sami wurin zama ne ya yi noma. Ina so ka yi masa halin arziki, ka lura da shi, ka ba shi gona da wurin da zai yi gida, domin yana da iyali suna zuwa daga baya."

Da ya gama ya ba shi. Makau ya yi masa godiya kwarai, suka yi ban kwana. Sarkin Kofa ya kira yaronsa, ya sa shi a hanya. Makau ya kama hanya ya yi ta tafiya har ya zo Makarfi. Ya tambayi gidan Tanimu, aka nuna masa, ya tafi ya ba shi takarda. Da Tanimu ya karanta ya yi masa maraba, ya saukad da shi a gidansa ya kawo masa abinci. Bayan da ya gama cin abinci sai ya ba shi dukan labarinsa.

Tanimu ya ce, “To, gobe idan Allah ya kai mu zan nuna maka gona. Akwai kuma wani gida inda gyatumata ta mutu kwanan nan, in zai yi maka sai ka gyara ka zauna a ciki."

Ya Aika Iyali Su Taho

MAKAU ya yi zamansa a Makarfi, ya yi ta noma, ya gyara gidansa ya sayi bayi biyu da kudinsa da ya tsinta, har ya soma arziki, ransa ya kwanta. Sa'an nan ya tafi wurin Tanimu, ya ce masa yana so ya aika iyalinsa su zo.

Tanimu ya ce, “Daidai ne, wannan shi ne muhimmi, gama dattijo kamarka bai kamata ya zauna babu iyali ba. Ni ma ina da wani yaro mutumin Kagara sunansa Isa, in ba ka da wanda za ka aika sai shi ya tafi."

Da aka kwana biyu sai Makau ya shirya tafiyar Isa. Ya sayi riga wurin Tanimu ’yar madaka kankararriya, ya kunshe ta cikin tsumma ya ba Isa, ya ce ya kai wa Sarkin Kagara. Kuma ya kawo wadansu ’yan tsaraba na Zazzau, ya ce a kai wa wadansu abokansa a can. Kuma ya ba shi marfiyu biyu, daya ya ba Sarkin Zagi, daya Sintili. Ya kawo ’yan kudi ya ba shi, ya ce ya rika saya wa mata abinci kafin su iso. Kuma ya ce masa, “A cikin matana akwai wata yarinya mutumiyar Fatika, da zan taso ta tambaye ni iznin ta je ta dubo iyayenta. To, in ka je ka samu ta tafi, ka bar mata sako cewa ta yi maza ta same ni tare da 'yan'uwanta a nan. Kuma in tana zuwa ta zo da danta maraya. Shi ke nan, Allah ya dawo da kai lafiya."

Ran da ya isa, bai zame ko ina ba sai fada. Ya tafi ya ba Sarki kyautar Makau, ya gaya masa abin da ya ke bukata na zancen iyalinsa.

Sarki ya ce, “To, madalla, a kai shi gidan Makau ya sauka har kafin ran da iyalinsa suka shirya, sa’an nan su tashi.“

Isa ya je ya sauka. Da la'asar ta yi sai ya aika wa Sarkin Zagi da Sintili da huhunan da Makau ya aiko musu, ya kuma ba da sauran tsaraba ga mutanen da Makau ya aiko shi gare su, suka yi ta murna. Bayan da Isa ya gama rabon wadannan kaya, sai ya shiga wajen iyalin Makau ya gaya musu dalilin zuwansa gare su. Suka yi ta farin ciki sai ka ce wadanda suka fada cikin ruwan Alkausara.

Sa'an nan Isa ya tambaye su, “Ina yarinyan nan mutumiyar Fatika, ko ta tafi ne ko ?“

Matan suka ce, “A’a, ga ta, da ma tana jiran aikensa ne."

Isa ya ce mata, “Makau ya ce ki tafi, amma ki hanzarta ki same shi a can. Kuma yayin da za ki tafi sai ki je tare da danki.”

Ta ce wa Isa, “To, daidai ne, Allah ya sa muna da rai, da kuma rabon ganawa."

Iyalan Makau suka yi kwana hudu suna kintsawa, sa'an nan rana ta biyar Isa ya tafi ya yi sallama da Sarki, kashegari suka tashi. Aka bam mu, ni da uwata, a Kagara. Bayan iyalan Makau sun tashi, sai kuma gyatumata ta yi shirin tafiya Fatika. Ana gobe za ta tashi, sai ta danka ni ga wani basakkwace sunansa Buhari, wanda ya ke makwabtaka da ubana mahaifi.

Tun da rana sai na ga uwata tana ta yawo a cikin gidaje, a ran nan ban yi tsammani ko bakin ruwa ma ta sha sosai ba, domin ba ta zauna ba ko kadan a wuri daya, sai dawainiya ta ke yi tsakanin gidajen kawayenta har dare ya yi. Bayan da ta gama yawace-yawacenta, sai ta dawo

gidan Buhari ta yi kwance tana ta kuka. Ni a lokacin nan babu abin da ya miskile ni ko kadan, sai farin ciki na ke yi, domin a gidan na sami yara 'yan‘uwana wadanda mu ke wasa tare.

An Kai Umar Riko

Bayan da dare ya yi, gari ya yi shiru, sai uwata ta tashi ta tafi wurin daya daga cikin matan Buhari, sunanta Amina wadda na ke dakinta, ta ce mata, “Amina, ina so mu yi ban kwana da ke yanzu, domin ina so zan tashi tun kafin a kira salla. To, sai fa ki dauki hankuri, kin san halin yaron, kullum abin da ya ke so ya yi in ba a bar shi ba sai ya yi kuka, amma idan ana barinsa ya yi abin da ya so a gaba ba zai ji dadi ba. Ya kamata ki rika kwabonsa ko yaushe, kada kuwa ki kula da cewa ai wannan yaro ba nawa ba ne, wallahi da ni da ke duk daya ne, tun da ya ke Allah ya hada mu, kuma a kan amana mu ke zaune."

Amina ta ce,' “Lalle dukan abin da kika fadi daidai ne, kuma ina fata Allah ya ba ni wuyan dauka.” Bayan wannan suka zauna suka yi ta tadi har mu yaran da ke dakinta muka yi barci.

Da suka jima kadan suna tadi, sai barci ya fara kama su, uwata ta tashi ta tafi ta kwanta, amma ko runtsawa ba ta yi ba domin tsananin tunanin abubuwan da su ke kan hanya kafin ta isa gida, da kuma tsoron da ta ke ji na wajen barina a garin da ya ke ba ni da dangin uwa balle na uba. Tana cikin tunanin nan sai ta ji carar zakara, ta tashi ta dauki kayanta ta kama hanya. Ashe kaddara ta riga fata. Ban sake ganinta ba sai bayan shekaru da yawa !

Wani Ya Sace Ni

DUKAN abin nan da ya auku ba ni da labari, ba kuwa ba ni da labari ba ne, don a sa’an nan ina da wajen shekara hudu ne kawai. Tunda uwata ta tashi daga Kagara ban ga wani abin da ya sake ba daga gare ni. Ina ci ina sha sosai, ga kuma yara wadanda mu ke wasa da su kullum. Ita Amina kuwa, matar Buhari wacce na ke gare ta, ba ta taba nuna mini wani mugun hali ba. Kullum abin da na yi duka daidai ne. In wani laifi na yi mata babba, yayin da ta zo za ta doke ni, in ta daga hannu sai ta fasa, ta ce, “Allah Sarki, yaro wawa !” Ba ta son in rabu da ita ko kadan, kullum tana

son mu zauna tare. Kuma yayin da na yi wani wawan kiwo nan da nan sai hankalinta ya tashi. Ta fita ta tafi gidajen yara wadanda ta san ina wasa da su, ta jawo ni.

Ran nan fa mun taru da yawa a kofar gidammu muna wasa, mu wajen yara tara, sai muka ga wani mutum mai babbar riga da babban aljihu yana zuwa ta ind mu ke. Dukammu muka bar wasa, muka zuba masa ido muna ta kallonsa har ya kawo gare mu.

Da ya iso wurimmu sai muka gaishe shi, "Sannu baba."

Shi kuma ya ce "Mai gidan na ciki ne "

Wani yaro daga cikimmu mai dan dama sai ya ce, "A'a, ya tafi bayan gari, amma zai dawo gobe."

Mutumin nan ya tsaya, ya yi ta kallommu muna Wasa, kana bayan zamani guda sai ya tambaye mu sunayemmu. Dukammu kowa ya fadi sunansa. Da ya ji sunana sai na ga ya tsaya kawai, ya kafa mini ido. To, duk daga cikin yaran kuwa ni ne karami. Ba a jima ba sai ya kira ni ya ce, "Sannu Umar, yanzu ka san ni dai ? Ina uwarka ta ke, ina ku ma babanka ? Zo mu je in kai ka wajen babanka, ka ji."

Na ce, "To."

Nan da nan sai na ga ya sa hannu a cikin wata 'yar jaka tasa, ya fid da soyayyen nama game da kudi biyu ya bani. Ka san al'amarin yaro, sai na karba ina tsalle. Ya kama hannuna muka yi ta tafiya, wai zai kai ni inda uwata da ubana su ke. Ni kuwa na yi ta binsa da kudina da namana a hannu, ina fincika. Muka yi ta tafiya yana kame da hannuna har dai muka fita bayan gari. Da muka isa bayan gari sai na ga ya ja ni mun shiga kwarin ganuwa. Muka yi ta tafiya har na gaji, Sai na yi kamar zan yi kuka, sai ya dauke ni a kafada ya dada mini nana.

Muka yi ta tafiya ina kan kafadarsa tun wajen azahar har goshin magariba. Su sauran yara wadanda mu ke wasa da su da ba su gan ni ba, sai suka fara yin kuka. Daga nan mutanen gidammu suka ji sai suka aiko wata kuyanga ta zo ta ga dalili. Da ta fito ta tambayi yara dalilin da su ke kuka, suka amsa mata wai Umar ne ya bata ba su gan shi ba. Suka ce kuma yayin da su ke wasa da rana, sun ga wani mutum mai babban aljihu ya zo ya dauke ni a kan wai zai kai ni wurin uwata da babana. Da kuyangar ta ji wannan sai ta yi salati ta sanad da Ubangji, ta shiga cikin gida wajen iyali don ta gaya musu abin da ya auku.

Da Amina ta ji sai ta fashe da kuka tana cewa, "Wannan abu ya kai gargara, lalle wani dan sane ya dauke Umar. Ni Amina wallahi yaya zan yi da raina ? In uwarsa ta dawo ba ta same shi ba, me zan ce ?" Sai ta fadi ta yi birgima tana kuka tana kururuwa har duk gari suka ji. Nan da nan sai aka buga gangami, kafin lisha ta yi duk daukacin namiji da ke garin yana bayan gari wajen nemana.

Amma ni da mutumin da ya dauke ni ba mu san abin da a ke ciki ba. Da dai ya ga dare ya yi, sai ya sauke ni daga kafadarsa, ya zaunad da ni a cikin wani dan kogon dutse, sa'an nan ya shiga. Ya fitad da nama da nakiya daga cikin jaka tasa ya ba ni, ya kawo ruwa ya ba ni na sha. Muka zauna a cikin kogon, a sa'an nan kuwa ban kula da kome ba, domin cikina ya riga ya cika. Shi kuwa nufinsa in huta kadan sa'an nan mu tashi.

Ina zaune, yana cin abinci, sai na ga ya tsame hannu daga abinci ya bar taunar wanda ke bakinsa, ya tsaya kawai kamar doki yayin da ya ji motsin wani abu. Ya dade cikin wannan hali sa'an nan ya tashi da sanda, ya durkusa a kan guyawunsa, ya leka waje. Ba a jima ba sai na fara jin maganar mutane arewa da mu. Da jin wannan sai na ga ya sa hannu a cikin jaka tasa ya dauko wata laya ya buge ni da ita a ka. Bayan wannan ya kwanto wuka daga cikin ratayensa, ya ce mini, "Ka ga wadan nan mutane sun fito yawo ne a cikin daji domin su kama yara su cinye. Watakila za ka ga wanda ka sani a cikinsu, amma fa kada ka yarda ko ya kira sunanka ka amsa, in kuwa ka amsa lalle ka tabbata zan yanke wuyanka da wannan wuka." Sai ya zaro ta ya nuna mini. Da na duba sai na ga tana walkiya walwal a farin wata, duk jikina ya dauki bari, nan da nan sai na tsunke da zawo.

Da masu nemana suka kusato kogon inda mu ke, sai wani daga cikinsu ya ce, "Kada mu wuce wannan wuri, domin da na sani a wajajen nan akwai wani kogo inda wata rana da muka fito

gudummuwa muka kama wani dan sane da ya sato yarinya. Sai mu je mu duba nan tukuna, in babu kome mu wuce." Duk abin da su ke fadi muna ji. Sai mutumin nan ya dauko wuka tasa ya aza mini a wuya, ya ce in na yi magana ko dan motsi ma lalle zai yanka ni.

An Yi Nema Ba A Gan Ni Ba

Mutanen nan suna zuwa suna tadi har dai suka zo bakin kogon da mu ke. Da zuwansu sai daya daga cikinsu ya kira sunana, "Umaru dan Makau !" (Domin shi ne sunan da Amina ta ke kirana da shi). Ya yi ta kira, ni kuwa ina ji, amma babu dama in amsa sabo da tsoron kaifi. Suka yi ta kira har suka gaji, babu wanda ya amsa musu, su kuwa ba wanda ya leka kogon balle ma ya shiga. Daga nan suka koma gida. Sauran mutane kuwa suka gauraye dajin, ko alamata ba su gani ba. Da suka gaji su ma suka kama hanyar gida. Suna tafiya suna cewa hakika uwar yaron nan in ta ji wannan lalle za ta yi hauka ko ta mutu.

Mutanen nan da suka isa gida sai suka gaya wa Amina, ba su same ni ba. Sai ta fashe da kuka, dukan mutane suka kewaye ta suna ba ta hakuri, cewa haka Allah ya kaddaro. Sai ta share hawaye ta shiga cikin dakinta. Amma da ta duba akushin tuwona d ta ajiye mini, da kuma inda na ke kwanciya, duk duniya ta zama baki sitik a wurinta. Sai ta fada a kan gado ta yi ta kuka ita kadai. Tun ran da na bace ba ta sami kwanciyar rai ba sai da ta hadu da uwata a Fatika.

Kura Ta Cinye Barawo na

LOKACIN da masu nemana suka koma tsakar dare ta yi. Da mutumin da ya sace ni ya ji daji ya yi shiru, sai ya ce da ni, "Yanzu mun huta ko ? Mu tashi mu tafi. " Sai ya dauke ni a wuya ya yi ta tafiya da ni a cikin daji har muka kawo wani dan gidan gona. Sa'ad da muka zo wurin asuba ta yi, sai ya sauko da ni daga wuyansa, ya ce ya gaji! Sai mu shiga cikin gidan nan domin ya yi rurumi. Ya ja ni, muka shiga tare muka kwanta, ba a jima ba sai barci ya share shi. Amma ni ba ni jin barci, domin na rigaya na yi yayin da na ke kan wuyansa. Da ma fara barcinsa ke da wuya, sai ya fara gwarti wanda har ya razana ni. Da ya saka ni a bayansa yayin da zai kwanta amma da ya fara gwartin nan tsoro ya kama ni, na tashi na shiga cikin wani kwando wanda masu gonar suka bari a dakin na yi zamana.

Ba a jima ba sai na fara jin gurnanin wani abu mai ban tsoro a bayan daki. Ashe gurnanin kura ce, da ta fito farauta ba ta samo kome ba har asuba, za ta koma kogonta, sai ta ji gwartin maigidana ta zago ta gani. Ka san yadda dakin gona ya ke, babu wani sayi mai aminci, ko tufaniya ma babu a kofar dakin da mu ke. Da kura ta zo kofar dakin sai ta tsaya, tana shawara ko ta shiga ne ko ta koma. Gari kuwa ya kusa wayewa.

Sai ta yi kuru ta kurma kai ta shiga, ta sami mutumnin a bakin kofa, ta tsaya a kansa tana jin ta inda numfashinsa ya ke fita. Sai na ga ta kafa masa hakori a makogwaro, ba wani jinkiri ko wahala, sai na ga ta raba kansa da jikinsa, misali kamar mutum ya sami almakashi mai kaifi ya datse ganye sabon toho.

Duk abin nan da kura ta yi mutumin bai farka ba. Ka san mutuwa yadda ta ke, kowane irin mai rai yayin da zai mutu sai an dandana masa zafi. Sabo da haka yayin da iska ta bugo mutumin nan dan ta wajen yankan nan, sai na ga ya fara shure-shure, kura kuwa tana jira. Da ya gama shure-shure sarai, ta tabbata ransa ya fita, sai ta suri uwar jikin ta saba a baya, ta nufi kogonta, ta bar kan a a cikin dakin tare da ni.

Gari ya waye, rana ta fito sai na tashi na fita waje. Na je gindin wata dorawa a cikin gonar, na zauna ina ta wasa da tsakuwa. Da hantsi ya dubi ludayi, sai na fara kuka, ina kira, "Baba, baba." Ba wanda ya amsa mini. Bayan da na dade ina kuka, sai na hango wadansu mutane suna zuwa, ashe masu gonan ne. Sai na dada kuka ban bari ba sai da suka iso gare ni. Yayin da suka zo suka gan ni yaro ne karami. Suka tambaye ni abin da ya same ni. Na gaya musu kaman nan, domin a lokacin ban san yadda za a ba da labari ba. Na ce, " Baba kula ci daji jiya a daddale, kansa cikin daki."

Bayan na fadi wannan magana saí wata mace daga cikinsu ta ce, "Ayya! Yana nufin wai ya ce ne jiya da daddare kura ta cinye babansa, ta bar kan a cikin daki."

Sauran suka ce, "Ai wannan kuwa ya zama gaskiya. Kai yaro, ina ubanka ?"

Sai na nuna dakin da na kwana. Nan da nan sai suka nufi wurin. Da dai zuwansu kofar dakin sai suka fara ganin jini a bango, sai ka ce saniya ce aka yanka.

Mijin Ya Zo

Muna cikin haka, sai ga mijin matan nan da mu ke tare da su ya zo ya same mu muna tsaye a kofar daki matan suna ta salati irin nasu. Da zuwansa sai suka habarta masa duka abin da ya auku, ya yi salati, ya dauki kan nan da kura ta bari, ya je bakin gona ya turbude. Bayan wannan sai ya ga tufafin mutumin ya shiga binciken abin da ke akwai. Da bude rigar mataccen sai ga wata babbar zabira, ba kome a ciki sai soyayyen nama, da dandakwarya, da garin soye, da wani dan koko. Kuma ya duba yar ciki sai ya ga wadansu layu guda biyu, daya an mata rufi da fatar goshin damisa da sasari a hancinta. Dayar kuwa da fatar minjirya aka rufe, aka dinke da jijiyar biri. Ita layan nan ta biyu kuwa a cikin wani yankin tsumman saki aka kunshe ta. A nan kuma ya sa kitsen mutum wanda ya ke milke ta da shi. Kuma tana hade da idon jinjiri.

In gajarta maka magana dai, da ya dudduba kayan mataccen nan sarai sai ya ajiye zuciya ya ce, "Lalle wannan mutum ba uban yaron nan ba ne, ba shakka ya sato shi ne daga wani wuri, domin wadannan kaya babu mai irinsu sai yan sane ko 'yan kwanto. Guzurin nan nasa kuma irin na masu sane ne."

Bayan ya fadi haka, sai ya juyo ya tambaye ni wadansu tambayoyi wadanda har abada ba zan iya tunawa da su ba. Ya yi ta magana a banza, ban kula da abin da ya ke fadi ba balle in ji. Ina ta wasan kasa abina tare da 'ya'yansa kanana.

An Sake Ba Da Ni Riko

Da ya ga ban mai da hankali gare shi ba, sai ya ce wa daya daga cikin matansa, "Wance, ke ce ba ki da da, to, ga shi Allah ya ba ki, sai ki rike shi, Allah ya sa na moriya ne." Ta durkusa ta yi godiya, kana ta dauke ni ta tambaye ni sunana, na fada mata ta yi murna.

Bayan wannan sai suka fada aikin gona, suka yi ta yi, mu kuma muna wasa har azahar ta yi. Sa'an nan suka taf rafi suka wanke jikinsu. Bayan da suka gama suka dawo gindin dorawa wajen da mu ke, suka zauna domin a sha ruwa, kana a tafi gida. Sai na ga wata ta bude wani masaki, ta fito da gaskami ta garwaya da gari, ta sa ruwa, ta ba kowa nasa. Mu kananan yara aka ba mu namu a ludayi muna lakuta da yatsummu.

Bayan da muka gama shan dorowan nan sai kowace mace ta dauki danta ta saba a baya. Ni kuma uwata ta dauke ni ta saba, muka kama hanyar gida. Maigidammu yana baya da kwari da baka a rataye, kuma kannensa biyu suna gaba da nasu kayan fada a rataye. Mu yara da mata muna tsakiyar su.

Mun rabu da gonar ke nan kadan, sai muka rika jin dirin dawaki cikin daji, da mutane suna cewa, "Kama hau, yau gadonku zai kwana wofi!"

Cikimmu duk ba wanda ya kula da abin nan da su ke fadi, sai ta tafiya mu ke yi. Amma ko da ya ke a cikimmu ba wanda ya nuna alamar ya kula, lalle kowa zuciyarsa ta raurawa, babu mai sauran laka a jikinsa, kowa sai jefa kafa ya ke yi. Muna dai ta jin sukuwar dawaki da maganar mutane, amma ba mu ga kowa ba.

Can an jima sai muka hango wani barde mai kilin doki ya sunke cikin sulke, ya sako ingarmansa bisa gare mu yana fadi, "Yau gadonku zai kwana wofi!".

Cikimmu duk ba wanda ya kula da abin nan da su ke fadi, sai ta tafiya mu ke yi. Amma ko da ya ke a cikimmu ba wanda ya nuna alamar ya kula, lalle kowa zuciyarsa ta raurawa, babu mai sauran laka a jikinsa, kowa sai jefa kafa ya ke yi. Muna dai ta jin sukuwar dawaki da maganar mutane, amma ba mu ga kowa ba.

Can an jima sai muka hango wani barde mai kilin doki ya sunke cikin sulke, ya sako ingarmansa bisa gare mu yana fadi, "Yau gadonku zai kwana wofi!"

Da jin haka sai maigidammu ya ce, "In Allah ya yarda kai ne gadonka zai yi hasara, domin watakila yau kan sabara, ka ke kwana"

Nan da nan sai na ga ya mika hannu a jikin kwarinsa, ya zaro wata fasa wadda har jikin kyauronta yabi ne, ya dana, ya durkursa yana jiran barden. Shi kuwa barden tun da ya sako doki bai zame ba. Maigidammu kuma yayin da ya ga ya yi kusa da shi, sai ya tattare jikin bakansa, ya sau masa kibiya. Nan da nan ya sa garkuwa tasa ya tare, kafin a ce maigida ya sami damar zaro wata kibiyar barden ya kade shi, ya bar shi rigingine sumamme kamar ransa ya fita.

A lokacin nan basira duk ta bace mana. Sai muka zuba ido kawai, muna kallon abin da aka yi. Kan a jima kadan sai muka ga dawaki wajen bakwai sun nufo mu a sukwane. Da ganinsu kowa a cikimmu ya sunkuya ya ranta cikin na kare. Duk sauran mata suka gudu suka bar uwata tana goye da ni ba ta iya gudu domin ta sare kafarta da masassabi.

Barde Ya Kama Mu

Da barden da ya kade maigidammu ya ga haka, sai ya sauko daga kan dokinsa, ya jawo uwata tare da ni a goye, ya hada da maigidammu, ya daure mu tam da asalwayin dokinsa. Sauran masu dawaki da dai suka ga haka, sai suka rufu a bayan 'yan'uwammu, ban san kuma yadda suka kare ba. Ga zatona dai sun kama su, domin ko wacce tana da goyo.

Bayan da barden ya kukunce mu, sai ya tasa mu a gaban dokinsa, yana tura mu zuwa garinsa. Muka yi ta tafiya har gari ya waye. Da safiya ta yi sai ya karbe ni daga bayan uwata, ya aza ni a a kwacciyar sirdinsa, domin ya ji tausayin uwata da te ke goye da ni. Muka yi ta tafiya wajen kwana uku, sai ga mu a Birnin Kano. Shi mutumin kuwa daya daga cikin manyan bayin Sarki ne, fatara ce ta kama shi ya fita dan yawo, domin ya zo ya sami abin bukata. Sa'ad da muka iso cikin gari babu wanda zai so ganimmu, saboda tsananin azaba game da bakin cikin.

Gyatumata Ba Ta Da Labari

DUKAN abin nan da ya auku gare ni gyatumata ba ta da labarin ko daya. Domin da ta kai Fatika ta tarar an kama ubanta a kan maganar maita, aka tafi da shi Zazzau. Tana can tana jiran dawowarsa, sa'an nan ta zo ta dauke ni zuwa Makarfi wajen Makau. Bayan ta yi wata biyu da kwana goma sha daya a garinsu, sai ubanta ya dawo daga birni. an sako shi, magana ta kare. Domin yayin da suka je shari'a, Sarki ya zagi manyan mutanen Fatika a kan sharrin da suka yi masa, ya ce babu wani abu wai shi maye a duniya. Amma fa Sarki bai yi wannan magana ba sai da uban uwata ya waka masa shanu biyu duka na tatsa. Yayin da zai fito Zazzau, Sarki ya hada shi da wani bafade su zo ya tafi da shanun. Suka zo tare da bafade aka ba shi shanun Sarki. Da aka ba shi ya ce, "A'a. Ni haka za a bar ni in tafi ? Nan da nan ba wani musu sai uban uwata ya kawo wata 'yar burguma ya ba shi, ya kora zuwa gida. Aka bar uban innata sai wata 'yar karsana, da wani bunsuru mai buzurwa har kasa.

Mutanen gida suka yi ta murna saboda mai gida ya dawo lafiya. Jama'a da yawa masu kaunarsa suka yi ta zuwa suna yi masa barka da kubuta. Bayan dukan masu zuwa sun tafi sai uwata ta iske shi a daki ta yi masa barka da arziki. Yayin da ta shiga dakin sai ta fashe da kuka, ka san irin farin cikin mata. Ya tambaye ta labari, duk ta habarta masa tun daga farko har zuwa karshe, ba ta manta da ko daya ba. A nan ya sa mata albarka, ya ce ta yi kokari, ta yi niyya, bayan yan kwanaki kadan ta koma Kagara ta dauko ni, sa'an nan ta zo ta wuce zuwa wurin Makau. Sai ta fara shirin tafiya. Bayan ta gama shiri ran nan ana kamar gobe za ta tshi, sai ta tafi wajen ubanta ta roke shi wani daga cikin 'ya' yanta ya raka ta.

Ya ce "Shi ke nan, ku tafi da Dabo." Aka kira Dabo, aka shaida masa zai raka inna Kagara. Bayan sun gama shiri wajen goshin a la'asar, sai ta dauki tulu domin ta debo ruwa a wata rijiya wace ta ke daf da hanyar fatake ta zuwa Kagara. Ta jefa guga ta debo ruwa ke nan sai ta hangi wadansu mata da rufin kai daga nesa da wani mai doki sun fito daga wajen Kagara. Nan da nan sai ta fitad da guga, ta tsaya kawai ta zuba ido har suka iso. Da isowarsu, sai ta ga mai dokin nan ashe Buhari ne. Da duba fuskokin matan sai ta sansance Amina. Sai ta yi wuf ta je ta rungume ta, tana kuka tana yi mata maraba. A nan ta gangarad da tulun, ta karbi kayan Amina, ta wuce gaba har zuwa inda Buhari ya sauka. Da ta ga saukarsu sai ta koma gida domin ta yi musu tanadin abinci. A lokacin ba ta lura ba ni cikin tafiyar ba.

Ta dawo gida, ta shaida wa ubanta dukan abin da ya auku, ta ce a yi mata abinci mai kyau wanda za ta kai wa bakinta. Nan da nan sai aka kama kaji biyu aka yanke, aka debo shinkafa daga rumbun uwa tata aka dake aka bushe aka wanke aka dandara tuwo da ita.

Almuru na yi, sai inna ta dauka ta tafi ta kai masaukin su Amina ta ajye, ta dawo gida ta ci nata. Bayan da ta gama jibi, kuma ta tabbata su ma a sun gama, sai ta tafi wurinsu domin ta ji labari. Da isarta ta samu Amina babu yadda ta ke, tana ta kuka, duk idonta sun kunkumbura. Da ta ga Amina cikin wannan hali, sai ita kuma ta koma waje daya ta tsuguna. ta yi tagumi.

Jim kadan Amina ta bar kuka ta share hawaye, suka gaisa. Sai inna ta tambaye ta dalilin da ta ke kuka.

Ta ce, "Babu kome."

Inna ta ce, "Ke dai in da wani abu ne ya faru ki gaya mini, barin kashi a ciki fa ba ya maganin yunwa."

Sai inna ta fara tsamnani a ranta ko Allah ya kiraye ni ne bayan tashinsu daga Kagara. Amina dai ta yi shiru, ba ta ce kome ba.

Suna cikin haka sai ga Buhari ya shigo domin ya gaisa da inna. Ya zo ya same su suna zaune zungum. Ya shiga ya zauna. Inna ta yi masa maraba, suka yi gaisuwa, ta tambaye shi labarin yadda ya bar Kagara, da inda ya ke nufin tafiya. To, ka san namiji. Sai ya ka da baki ya ce mata, "Kagara lafiya. Yanzu na yi niyyar zuwa Hausa in ziyarci kabarin babban waliyyi, Shaihu Usumanu dan Hodiyo. Bayan wannan ina da bukata in je in dubo wadansu kawunnaina a Tureta, daga nan kuma in wuce zuwa Dingyadi wajen gyatumata, domin mun dade rabommu da juna. To, bayan wannan sabili da ke na biyo ta wannan gari domin in shaida miki abin da ya auku bayan tashinki daga Kagara. Yaron nan dai bayan tashinki da kwana tara, wani dan sane ya sace shi. Aka yi ta nema da gaske, ba a ji motsinsa ba. A lokacin kuwa ni ma ba ni gida, na tafi kauye, domin in dubo wani abokina mara lafiya. Da na dawo na tarar da wannan labari. Amma mun ji labari daga

wajen wani wai shi Amadu cewa lalle ya ga Umar a Birnin Kano a gidan wani babban bawan Sarki wanda a ke kira Gumuzu, kuma ya ce ya ji shi Gumuzun da wani Balarabe ma sunansa Abdulkarim suna magana wai yana son ya fanshi yaron, ya tafi da shi can wajen kasar Masar ya ba mata tasa, watau ya zama kamar dansa. Wannan labari fa shi ne wanda zan iya gaya miki na game da Umar, shi ne kuma dalilin da ya sa na biyo ta wannan gari. To, yanzu sai ki dauki hakuri bisa kaddarar Allah, kuma ki tuna a ranki hakuri ya fi kome.'"

Innata ta yi jirim kawai. Bayan zamani mai tsawo ta ce, " To, mutum duk na duniya in bai yi hakuri ba lalle ya ga bacin rai dubu. Allah ya sawwaka."

Da Buhari ya gama gaya mata wanan labari sai ya fita waje, ya bar ta da Amina su yi tadinsu. Suka yi tadi har can tsakad dare, sa'an nan inna ta taso ta dawo gida. Da isowarta ta shaida wa uwarta da ubanta abin da ya auku. Su kuma dukansu suka ce, "Allah mai iko !"

Da gari ya waye sai inna ta koma wajen su Amina domin su yini. Yayin da ta ke can sai ga wani kanenta ya zo a guje, wai an aiko daga gida ya kira ta, ta yi bako daga wajen Zazzau. Sai ta yi farat ta tashi ta tafi gida ta sami Isa ne, mutumin da Makau ya aiko shi ya tafi da iyalinsa Makarfi. Ta marabce shi, ta kawo masa ruwa ya sha. Ta tafi ta shaida wa ubanta cewa yaron mijinta ne. Nan da nan aka share masa daki, ta kai shi. Bayan da ya zauna ya huta kadan, sai ya ce mata, "Kin shaida ni dai ?"

Ta ce, "Ai har in mutu ba ni mantawa da kai".

Ya ce mata, "Makau ne ya tsananta yana so ki yi gaggawa ki koma ki same shi tare da yaron nan. Ya ce nan da nan mu tafi ga sawuna ga naki"

Inna ta ce, "To." Sa'an nan ta habarta masa dukan abin da ya auku bayan rabuwarsu. Isa ya yi ta mamaki bisa hukuncin Ubangiji.

Da suka gama wannan zance, sai ta dauke shi zuwa wurin iyayenta don ya fada musu sakon Makau da bakinsa. Isa ya shaida musu kome, sa'an nan ya koma dakinsa ya yi kwance sabili da zafin ranar da ya dauko. Ita kuma bayan da suka rabu da Isa, sai ta koma wajen su Amina tana murna. Ta shaida musu abin farin cikin da ya same ta. Dukansu sai suka yi ta farin ciki har suka kusa mantawa da bacewata. Da inna za ta koma gida, sai suka yi ban kwana da su Amina dayani domin su da asuba za su tashi. Da suka gama ban kwana sai ta koma gida. Asuba na yi sai su Amina suka tashi suka nufi Kasar Hausa.

Inna dai daga komowarta gida ba ta yi wani dan jinkiri ba sai ta fara shirin tafiya wajen mijinta. Bayan su Amina sun tashi da kwana biyar, sai inna da Isa su kuma suka tashi. Suka yi tafiyarsu cikin kwanciyar hankali, bayan kwana hudu ran na biyar sai ga su a MaKarfi.

Yayin da suka zo sai suka iske Makau ba shi gida, ya tafi gewayar wata sabuwar gonarsa, a bayan gari. Isa ya tura inna cikin gida wajen 'yan'uwanta mata, shi kuma ya tafi gida ya yi wanka ya sake tufafinsa. sa'an nan ya fito ya tafi wajen Makau a bayan gari, ya gaya masa ya dawo lafiya. Makau daga wurin da ya ke zaune bai ko dan dakata ba, nan da nan sai ya garzayo gida. Ya iso ya shiga cikin gidansa yana mai dariya yana farin ciki da zuwan matarsa. Ya nuna mata daki ta shiga.

Bayan ta huta, hankalinta ya dawo, ba abin da ya fara tambayarta sai labarina. Ta gaya masa na bace. Bayan Wannan ya yi mata tambayoyi, ita kuma ta kwashe dukan abin da ta sani ta shaida masa. Daga nan sai tsoro ya kama Makau, duk ya kidime.

Wadannan abubuwa fa su ne suka auku ga uwata. Amma bayansu duka sai ta tsaida zuciyarta, ta sani Allah daya ne. In Allah ya so sai ta dangano da inda na ke, in ba mutuwa ta yi ba.

An Sayad Da Ni Ga Balarabe

A ZAMANIN da Gumuzu ya kamo mu, akwai ayari na Larabawa a cikin Birnin Kano, wadanda suka zo su sayi bayi su kai Kasarsu. Yawancinsu kuwa su kan yi abota da manyan bayin Sarki, domin in sun zo kullum su ne su kan yi musu hanyar samu bayi. Ba kuwa ko yaushe su ke zuwa

ba, akwai ajiyayye lokacin zuwansu. Kuma kullum yayin da suka zo suka sayi bayi, in za su tashi su koma kasarsu su kan yi alkawari da abokan nan nasu, su tara musu wadansu bayi kafin su sake dawowa. Cikin Larabawan nan Gumuzu yana da wani aboki ana kiransa Abdulkarim na wani gari cikin Kasar Masar.

Ran nan muna zaune bayan mun shekara biyu cur tare da Gumuzu sai na ga wani mutum fari dogo, mai dogon gemu da gashin baki, ya taho gare shi. Da zuwansa sai na ga Gumuzu ya tashi daga kan shimfidarsa, ya zaunad da shi a kai, yana ta ce masa, Maraba, sannu da zuwa ! Bayan sun gama gaisuwa sai ya kira ni ya ce in je cikin gida in karbo wa bakon nan ruwa. Na shiga na kawo masa ruwan surki mai zuma. Na zo na durkusa gaban bakon nan, na mika masa ya karba ya sha. Bayan ya sha ruwa ya yi hamdala, sa'an nan ya juya wajen Gumuzu ya tambaye shi, "Yaya, ban san wannan yaro ba, danka ne ?"

Gumuzu ya ce, "A'a, ka ji ka ji yadda na same shi, da ubansa da uwa tasa gaba daya".

Suka yi ta tadinsu, ni kuma ina tare da su har lokaci mai tsawo, sa'an nan kowa ya koma gidansa. Gidan bakon nan kuwa kusa ne da na Gumuzu. Sarki ya ba shi wurin farkon zuwansa, domin lokacin da ya zo duka ya sauka. Sa'ad da aka yi abinci duk sai a dora mini in kai masa masaukinsa. Har dai ya zama muka saba da shi kwarai saboda abincin da na ke kai masa kullum. Wani lokaci In na kai masa, ya kan tambaye ni ko ina sonsa. Ko yaushe na tafi sai ya kama ni ya shasshafa kaina yana sa mini albarka. Wani lokaci kuwa in zan komo gida ya kan kawo dabino da wani irin abinci ya ba ni.

Haka ya yi ta yi mini har wajen kwana goma sha shida. Ran kwana na goma sha bakwai sai na ga Gumuzu ya dauke shi sun nufi wajen fada. Da za su tafi kuwa Abdulkarim ya tambayi Gumuzu in ya yarda in jo in zauna masa a daki wajen kayansa kafin su dawo. Gumuzu ya kira ni ya shaida mini. Na tafi gidan Abdulkarim na yi zaune a dakinsa, su kuma suka tafi. Tun fitarsu da safe ba su dawo ba sai bayan sallar azahar. Ina cikin zamana a dakinsa sai na fara jin hayaniyar mutane da muryar Gumuzu. Kan a jima kadan, sai na ga Abdulkarim ya shigo cikin daki. Na yi masa barka da zuwa, shi kuma ya ce mini, "Shi ke nan. Tafi gida".

Da fitowata daga dakinsa, in dai duba haka, sai na ga bayi cikin kangi an shanya su kawai a rana. Da na dada dubawa cikin bayin nan, sai na ga uwata da uban nan nawa, wadanda aka kamo ni da su daga gona. Daga nan sai zuciyata ta karai, tsorona kuma a ya yi yawa. Ai da na ga haka sai na sunkuyad da kai na wuce, hawaye yana zuba a idona. Na tafi gida, aka ba ni abinci, ga shi ina jin yunwa amma dole na bar shi. Ba abin da na ke tunani sai bayin nan. Yayin da duk na sunkuyad da kai sai in gan su. Kai, na dai zama sai ka ce wanda aka kawo masa labarin ubansa da uwa tasa sun mutu. Na dame, duk na rasa abin da ya ke mini dadi cikin duniyan nan, yo ai dole sai na tafi dakin uwar goyona na yi kwance sai ka ce wanda ciwon ajali ya kama shi. Na yi kawai, na daga kaina ina duban rufin daki ina ta tunani."

Yayin da Ina cikin ninkayar tunanina, sai na ga mai gida Gumuzu ya shigo cikin gida. Da shigarsa kuwa sai na ji ya kama sunana, ina Wane ? Ni kuwa da jin haka, sai na yi firgigi na tashi, na ce, "Ga ni."

Na tafi gare shi, ya kama hannuna ya ja ni zuwa wajen gidan da Abdulkarim ya sauka. Muka zo muka shiga cikin gidan muka iske shi yana karatun Alkur'ani cikin Suratul Bakarati. Da shigarmu sai ya rufe littafi, ya ce wa Gumuzu, "Har ka same shi ?"

Ya amsa ya ce, "Ai ko da ma shi ba mai yawo ne ba kamar Sauran yara."

Daga nan sai suka shiga maganganu wadanda ba ni iya ganewa sosai, wadansu na kan ji, wadansu kuwa kamar yare ne. A karshen maganarsu sai na ji Gumuzu ya ce, "Abdulkarim, ai ka cuce ni da ka raba ni da wannan yaro, domin tun da na ke ganin yara ban taba ganin mai hankali mai lura da kansa kamar wannan ba. Gama ka ga tun ran da Allah ya sa na zo da shi gidan nan ban taba jin wata daga cikin matana, ko wani nawa, ya ce tir da yaron nan ba."

Abdulkarim ya amsa, "Irin wannan hali shi ne Larabawa su ke so, mutum na duniya duka in ba shi da hali ko shi wane ne, ko Fari ko Rawaya ko Baki, kamar dabba ya ke. Domin hankali da basira da hikima ba su tabbata daga cikin kome sai daga kyakkyawan hali."

Da jin wadannan maganganu fa, sai na fara sakawa a raina cewa, "Lalle ba shakka Abdulkarim zai tafii da ni kasarsu.

Ina cikin sakar zuci sai Gumuzu ya juyo gare ni ya ce, "Umar, ga Abdulkarim ya roke ni arziki yana sonka. Son nan kuwa da ya ke maka ba wai ka zama bawansa ne ba. Yana so in ka dauka a ranka, ka ga za ka iya zama da shi, ka zama dansa gama ba shi da da, ko dan dangi ma babu a gare shi. Ni na yarda ku tafi tare da shi yanzu yardarka ce kawai mu ke jira."

Bayan wannan sai na daga kai kawai ina duban nisan kasarsu Abdulkarim, kuma ina tunawa gyatumata tana da rai ba ta ma san ta inda Allah ya shilla da ni ba. A wurin fa sai duniyan nan ta taru ta yi mini baki kirin, ban san sa'ad da hawaye ya zubo mini ba. Da ganin haka sai Abdulkarim ya tambaye ni wai ko ba ni sonsa ne ? Ni kuwa na amsa masa ba haka ba ne, ba ni so ne in rabu da kasarmu. In na bi shi yaushe zan dawo gida ? Shi kuma ya ce mini kowace shekara in zai zo lalle zai zo da ni domin in duba mutanen kasarmu.

Na ce, "To, na yarda." Don kada su ce na cika rashin kunya bayan kuwa da sun yabe ni. Bayan da aka gama wannan magana sarai, na yarda, sai Gumuzu ya ce mini in koma gida. Da na tashi zan tafi sai Abdulkarim ya kawo kantu babba ya ba ni game da wadansu dabinai kekasassu wadanda babu irinsu ga zaki.

Sai na durkusa na karba, na mike tsaye na kunshe su a cikin babban bantena na saki, wanda Gumuzu ya saya mini. Na fita na kama hanyar gida. Na isa gida duk raina a bace, sai na tafi wurin uwar goyona na zube mata a kan mawanka na koma jikin shamaki na takure, na gama kai da gwiwa, na zama dai abin tausayi ainun. Da ganin haka sai ta fashe da kuka tana ta tambayar abin da ya same ni. Ni kuwa na habarta mata labari tun daga farko har karshe. Ta yi ta kuka tana cewa, "Babu kome, Umar, kai dai ka rike a ranka Allah shi ne Sarki."

Muka yi ta tadi har Allah ya sa Gumuzu ya shigo ya fada mata da bakinsa zan tafi kasar Masar tare da wani Balarabe abokinsa. Ta ce "To, Allah ya ba mu jinkiri dai."

Ya ce, "Amin."

A kwana a tashi ran nan bayan an yi wannan magana da kwana goma sha bakwai sai Abdulkarim ya yi niyyar tashi. Domin ya rigaya ya shirya sarai, bukata tasa duka ta biya, ya sayi bayi iyakar sayensa. Ban da bayin nan kuwa ya sayi wadansu guntayen bakaken rawuna da bakaken zannuwa da makamantansu don guzurin hanya. Bayan ya gama shirin nan nasa sosai, ana kamar gobe zai tashi, sai ya aiko aka kira ni na tafi, ya shaida mini cewa ya gama shiri, gobe zai tashi da sassafe, in je in yi sallama da abokaina da kuma iyayena mata, watau iyalan Gumuzu.

Na ce, "To." Na tashi na koma gida na yi wa dukan jama'a ban kwana, sa'an nan na kunso 'yar tabarmata a hammata na nufo gidansa, domin in kwana can kada in makara. Na same shi a zaune wajen la'asar, bayan ya kirga bayinsa ga kuma wadansu a daure guda goma dabam wadanda Sarki ya aiko masa da su sallama tasa. Dare ya yi muka shiga daki da shi, muka kwana kan shimfida daya har asuba ta yi.

Mun Fita Birnin Kano

ASUBA na yi sai na ji ana busa wani abu kamar kaho, kuma ana buga kuge. Dajin wadannan sai na dimauce na tashi a firgice, na ta da Abdulkarim na gaya masa. Shi kuma ya ce mini wai wadannan alamomi ne na matafa, watau sauran 'yan'uwansa sun shirya ke nan za su tashi. Ai nan da nan sai ya bude kofa ya fita, ya je ya jawo wani farin rakuminsa mai tozo biyu. Sa'an nan ya tafi shamaki inda bayin nan su ke shanye a filin Allah kamar tumaki, ya tashe su, muka mika.

Muka fita Birnin Kano da asuba ranar Asabar, uku ga watan Ramalan, sa'an nan hijirar Annabimmu Muhammadu (sallallahu alaihi wa sallama) tana da shekara dubu da dari uku dai dai. Dukan masu zuwa kasar Masar sai da suka hallara a kofar gari tukuna. Na manta da sunan kofar yanzu. Da aka gama taruwa kaf sai aka ba da alamar tafiya. Kafin mu tashi daga kofar, Sarkin Kano ya aiko mana da masu dawaki wajen hamsin domin su raka mu.

Da za a tashi sai maigidana ya kira ni ya dauke ni ya dora ni a gabansa a bisa kan rakuminsa. Muka yi ta tafiya, ni ban san jihar da mu ke nufa ba, har rana ta fito ta fadi ba a sauka ba. In dai gajarta maka, tun tashimmu daga Birnin Kano ban ga mun kwana wani gari ba sai Birnin Kuka. Da muka nausa daga Kuka dai ba mu tsaya ba sai a wani sarari mai yawan yashi. Ba gida ko daya a wurin sai wadansu alamu kawai na bukkoki, a nan ne ayari su ke tsayawa su shirya su debi ruwa kafin su shiga cikin babbar hamada. Muka kwana biyu, ba abin da Larabawan nan su ke yi sai gyare-gyaren kayan fada, kuma ana ta debo ruwa a salkuna ana ta labta wa rakuma. Kafin mu tashi sai wani Balarabe tsoho ya zo wajen Abdulkarim yana fada masa, ya shaida wa mutanensa su shirya, domin inda za mu shiga wuri ne mai hadari. Daga nan fa sai na fara jin tsoro, na yi tunani cewa ko za su yi yaki ne, shi ya sa na ga sun gyaggyara bindigoginsu da takubbansu.

Bayan an jima kadan sai aka buga kuge, duka muka tashi gaba daya da la'asar, muka shiga cikin babbar hamada. Kai! Cikin hamadan nan na ga abin mamaki, na kuma ji tsoron Allah, na gaskata cewa abin nan da zaki ya ke fada wa kura gaskiya ne, "Dan Adam abin tsoro."

Tun da muka fara shiga cikin hamada ban ga wata bishiya mai girma ba, inda duk ka duba sai ka hangi iyakar ganinka ba ka ganin kome sai yashi. Ba ruwan sama, balle wata ni'ima ta samu a wurin. Akwai iska, amma ba irin ta wannan kasa ba. Iskarsu ba ta tare da kome ban da yashi.

Mutum duk wanda ya san yadda iskar hamada ta ke ba zai yi kwadayin ta same shi ba a cikinta. Daga can dai in iska ta taso in ka duba sai ka ce hadari ne. Wani Balarab abokina ya ba ni labari cewa wani lokaci in iskan nan ta sami ayarin mutane sai ta gigita su su rasa hanya, duk su fantsamu cikin yashi. Kuma kome girman hanya a cikin hamada yayin da iskan nan ta bi ta wurin sai ta bace. To, da fa muka shiga wannan wuri tausayin bayin nan ya kama ni. Yayin da duk na dube su sai in gan su suna tafiya cikin yashi tubus tubus, duk gindinsu na baya-baya. Kai, ka san abin da wahala a ce mutumin da ya saba da tsadari ya yi tafiya cikin yashi.

Haka muka yi ta tafiya cikin yashin nan kwana da kwanaki. Kai, kada dai in kai ka da nisa, tun da muka tashi daga inda muka tsaya muka debi ruwan nan ba mu sake samun ruwa ba sai bayan mun yi kwana uku tukun kana muka sami wani dan gari na wadansu Bugaje a bakin wadansu 'yan kananan rijiyoyi a cikin yashi. A wannan gari ne fa na ga abin mamaki. Duk mutanen garin yaro da babba kowa yana da nadin bakin rawani misalin kamu uku. Daukacin wanda ka gan shi

da nadi kuwa duka ba shi da hula. Yawancinsu kuwa in sun yi nadi sai su jawo rawanin su rufe fuskarsu da shi. Matan garin kuwa ko wacce ce daga cikinsu tana da wani dan kyalle wanda ta ke rufe fuskarta da shi. Su irin mutanen nan na ji labari mafadata ne da gaske. Ni kuma da kaina na ga alamar haka da jin magana tasu, gama kowace magana su ke yi sai ka rika jinta fada-fada.

Mun Taba Ciniki

Yayin da muka iso garin nan da na fada maka, sai muka tsaya a bakin rijiyoyin, muka debi ruwa muka sha kowa cikimmu ya yi wanka. Bayan an jima kadan sai na ga mutanen garin mata da maza suna barkowa zuwa gare mu. Kuma in duba haka sai na ga kowane bafatake daga cikimmu ya kwance kayansa ya fito da bakaken rawuna da zannuwa irin wadanda a ke yi a Kano. Daga nan kuma sai na ga wurin duk ya hargitse sai ciniki a ke yi. Fataken nan suka yi ta ciniki har rana ta yi sanyi, zuwa can wajen la'asar sai na ga kowa ya kama kayansa ya daure. Da almuru ta fara kusatowa sai kuma aka buga kuge muka tashi.

Muka yi ta tafiya cikin hamadan nan, ba mu fita cikinta ba sai bayan wata biyu da kwana takwas. Ran nan fa bayan mun dibga tafiya mai tsanani sai ga mu a wani gari cikin kasar masar a yamma da Kogin Nil, wai shi Ber Kufa. Garin fa nan ne garin su Abdulkarim, inda zan zauna har shekara da shekaru. Da muka kusa isowa sai Abdulkarim ya ce mini garinsu ke nan, gidansa kuma yana kusa da inda na ke hangen nan. Mu gusa kadan sai ga mu a cikin gari wanda ban taba ganin irinsa ba tun da uwata ta haife ni. Da shiga garin bayan mun wuce gida uku sai muka kawo gidan Abdulkarim. Muka sauka a wurin da bayinsa, saura kuma suka wuce zuwa gidajensu.

A lokacin nan bayin sun rigaya sun gaji tibis aka kawo musu ruwa da abinci, amma ba su iya taba ko daya ba sabo da gajiya. Ni da isowarmu sai Abdulkarim ya dauke ni zuwa wajen matarsa ya ajiye ni, kana ya fito. Bayan da bayin nan suka huta sarai, hankalinsu ya dawo jikinsu, sai suka fada wa abincin nan, sai ka ce fara ta sami gona inda dawa ta fara tsirowa ta fada da figa. Abdulkarim ya zauna a wajen bayin nan har suka gama cin abinci sarai , kana ya shigo gida ya same mu muna zaune da matarsa, muna tadi da Hausa, domin ta iya. Dalili kuwa tun sa'ad da ya fara ciniki da Kasar Hausa ya taba zuwa da ita, suka yi wajen shekara uku a Kano. Ya shigo ya ba ta labarina sarai, ya gaya mata dukan abin da ya yi nufi da ni. Sai ta yi murna da gaske.

Bayan an kwana bakwai na saba sosai da matar Abdulkarim, ai ran nan ya ce yana so ya je bakin teku, don ya sayad da bayinsa. Da can ma ya taso da bayi tamanin, amma ashirin da biyar sun mutu a hanya. Kafin ya tashi sai ya ce wa mata tasa bayan ya tafi yana so ta kai ni wajen wani malami makwabcinsa in rika karatu. Ni kuma ya kira ni ya gaya mini haka, kana ya tashi. Ran da ya tashi da safe, da yamma ta yi mata tasa Zainab ta tafi da ni wajen Shaihu Mas'ud, wanda zan yi karatu a gare shi. Ta habarta masa duka abin da maigidanta ya fadi. Da ta gaya masa haka sai muka dawo gida tare, ta ce ba zan fara karatu ba sai gobe, in Allah ya sa muna da rai.

Kashegari da sassafe ta ba ni sabuwar riga da hula da wando, da kuma abin kalaci. Bayan na karya kumallo sai ta ce in yi niyyar zuwa makaranta. Na fita na tafi gidan Shaihu Mas'ud, na fara karatu. Kai, ya zama dai har in na fara karatu ba ni ma son zuwa gida ko kadan sai don abinci. Ban jima ba ina karatun sai abin ya zama mini kamar dara, gama ko ina na ke sai ka ji ina yi. Kafin wata guda ai sai allo. Kafin Abdulkarim ya dawo daga bakin teku ina iya yin harda daga Alhamdu har zuwa Sabbi.

Ran nan bakwai ga wata, ana cika ciki saura kwana uku, sai Abdulkarim ya dawo. Da zuwansa Zainab ta ba shi labarina, ya yi murna ainun, ya sa aka kama rago aka yanka, aka yi mini sadaka. Daga ran nan kome na ce ina bukata nan da nan sai a ba ni. Babu irin tufafin da ban sa ba.

Da shekara ta kewayo, Abdulkarim ya yi niyyar komawa Kano. Ya ce za mu tafi tare bisa ga alkawarin da ya yi mini. Da na ji haka na kosa lokacin ya yi in je in gano kasarmu. Bayan da muka shirya duka, sai aka kawo masa labarin abin da ya faru cikin Kasar Sudan. Shi ne Muhammad Ahmad ya tayar wa Kasar Masar, ya ce wai shi ne Mahdi. Mutanen Kasar Sudan duk suka bi shi. Aka aika masa da yaki daga Masar. (Domin jin labarin wannan Mahdi, sai a nemi wani littafi mai suna ABDULKADIR SALADIN. Za a iya samun littafin a shafin Taskar Bukar Mada - http://bukarmada.blogspot.com )

Da Abdulkarim ya ji haka ya ce gara mu dakata mu ga abin da zai faru, domin hanyar da za mu bi ke nan. A sa'ilin nan kuwa kowa yana tsammani abin ba zai dade ba, nan da nan za a a gama mu tashi. Muna cikin haka sai aka kawo labarin yaki ya baci. Jama'ar Mahdi suka yi nasara, dukan Kasa ta yamutse. Aka sake aikawa da yaki daga Masar, abin ya rigaya ya shaddada. Da muka ji haka babu damar tafiya, tilas muka zauna.

Ka san halin yaro, yau da gobe sai na fara mantawa da kasarmu, da dangina, har da uwata. Na yi ta karatu har wajen shekara biyu na sauke. Na sauke Alkur'ani ranar Laraba sha daya ga watan Muharram. Ran nan an yi biki wanda watakila ba zan sake ganin kamarsa ba. Da sassafe aka kama shanu uku aka yanka, aka soke rakuma biyu, aka yanka tumaki da talotalo wajen tara. Abincin da aka yi a gidammu da kuma wanda aka kawo gudummuwa ba shi da isani. Abdulkarim ya shiga cikin soronsa ya fito da riga irin ta Larabawa tabbatacciya mai walkiya kamar azurfa, da wandon Tunas wanda aka yi masa aiki har kubaka, da wata irin zulaika ta alharini, da hulad dara mai tuntun farin alharini, da rawani rawaya. Dukan kayan nan ya ba ni in sa. Da na sa ya ce in wuce gabansa zuwa makaranta inda gaggan malamai suka taru, domin in zo in yi 'yar takara su ji, kana su yi mini addu'a. Na wuce gaba har muka zo makarantar. Muka zauna, kowa sai dubana ya ke kawai yana mamaki. Shaihu Mas'ud sai ya zo da wadansu takardu warka biyu na Alkur'ani ya ba ni in karanta domin shaida. Kowa fa sai ya ja ya yi shiru, aka kasa kunne kawai, ni kuma na fara karatu. Na karance takardun nan sarai, babu ko dan garma-garma. Da na gama sai duka wurin aka dauka Alhamdu Lillahi. Aka yi mini addu'a, sa'an nan aka shiga rabon abinci.

Bayan na sake sauke Alkur'ani da kwana kadan sai maigidana Abdulkarim ya kawo wadansu littattafan ilmi ya ba ni, game da wadansu kuma na addu'o'i da na magunguna. Na karba na tafi da su wurin Shaihu Mas'ud. Yayin da na kai masa ya karba ya zuba bisa shimfidarsa, ya dauko daya ciki wai shi Ashmawi ya ba ni, ya ce da shi zan fara, domin kuwa shi ne littafi na farko wanda ya ke koya wa mutum batun addini sosai. Na Shiga wannan littafi, kafin a ce me na rigaya na sauke. Kafin 'yan shekaru kadan sai na zama kusan na biyu bayan Shaihu Mas'ud a Birnin Ber Kufa. Daga nan fa sai mutane suka fara kirana Shaihu Umar. Mutane da yawa daga biranen Masar suna zuwa su ziyarce ni. In sun zo sai su yi mamaki cewa ga ni Baki, amma Allah ya ba ni basira da fahimta mayawaita. Ana cikin haka sai Shaihu Mas'ud ya rasu, ba wata tantama sai aka sa ni a matsayinsa na limanci, dukan almajiransa kuma ya zama ni na na ke ba su karatu.

Gyatumata Ta Tafi Nemana

AMMA a can kasarmu gyatumata tun da aka ba ta labarin an sace ni hankalinta bai kwanta ba da kome na duniya. Yayin da duk ta zauna ita daya sai ta rika fadi a cikin ranta cewa in Allah ya yarda garin da duk na ke sai ta je. Tun da muka rabu ba ta ci abinci ya zauna mata ba. Ta kare, ta

rame ta zama fara sol kamar fatalwa, duk ta fita haibarta. Makau ya yi mata abu da yawa domin ta manta da tunanina, amma babu dama, har dai ya gaji ya daina.

Ran nan fa bayan na rabu da ita kamar shekara daya, sai ta tashi ta ce wa Makau ya ba ta izni ta je duk inda na ke cikin duniyan nan ta dubo ni. Da farko Makau bai yarda ba, amma da ta tsananta ya yarda. Ya kawo kudi da tufafi masu yawa ya ba ta, ta tashi ta tafi Kano. Da isowarta birni, sai ta tambayi gidan Gumuzu, aka kai ta ta sauka. Ta tambaye shi labarin inda na ke ya gaya mata, bai boye mata kome ba. Ya gaya mata sunan kasar da na ke ciki, da garin, da sunan maigidana. Da ta ji wannan labari ta ajiye zuciya, ta yi hamdala, sa'an nan ta tambaye shi yadda za ta yi ta tafi can inda na ke.

Gumuzu ya amsa mata cewa, “Lalle kin zo cikin sa'a, domin wadansu ayari za su tashi zuwa can kafin kwana uku. Amma fa ayarin kashi biyu ne, daya za su tafi Murzuk, daya kuwa inda danki ya ke."

Bayan sun yi wannan magana da kwana biyu, sai ta tashi ta tafi kasuwa tana tambayar inda ayari masu tashi gobe su ke. Aka nuna mata wajen ayarin masu zuwa Murzuk. To, a cikin ayarin kuwa akwai wani attajiri na Birnin Kano wanda zai tafi can wai shi Ado. Da zuwanta wajen da ayarin nan ya ke, sai ta tafi gabansa ta durkusa, tana tambayarsa zancen tashi. Shi kuma ya gaya mata gobe, sa'an nan ya tambaye ta, “Ke ma za ki shiga cikin tafiyar ne ?"

Ta amsa masa, “I, ina so ne inje in sami dana wanda ya ke a wani gari wai shi Ber Kufa cikin kasar Masar."

Da Ado ya ji wannan, sai ya kulla a ransa ya cuci gyatumata su tafi tare, ya mayar da ita Kamar matarsa, a cikin matarsa kuwa kuyangarsa. Ya ce mata, “To, ai wannan daidai ne, sai ki je gida ki debo kayanki. Amma dai Allah ya yi maki sa'a tun da ya ke kin samu ina cikin wannan tafiya. Sai ki zo ki zauna tare da ni, har sa'ad da Allah ya kai mu can, gama ta garin da kika fadi ta nan ne za mu bi."

Da uwata ta ji wannan magana sai ta koma masaukinta, ta debo 'yan kayanta ta danka masa a hannu da cewa ta zama amanarsa da ya ke Allah ya hada su haka. Bayan ta kawo masa kaya da yamma, da asussuba suka tashi. Suka yi ta tafiya, su kwana wannan gari yau, gobe su tashi, da haka har suka isa Ghat. A wurin fa suka yi niyyar kwanaki da dama sabili da ciniki. Har yanzu uwata ba ta san abin da Ado ya ke nufi da ita ba. Sauran mutane kuwa da suka gan ta tare da shi suka zaci mata tasa ce, domin kuwa sun ga a kan hanya yana nuna alamar yana kishinta.

Ana kamar gobe za su tashi, ran nan Ado ya tafi kasuwa domin ya sayo wadansu kayan guzuri, sai uwata ta sami wata Bakanuwa baiwar wani Balarabe. Suka zauna suna tadi sai ta tambayi uwata dalilin fitarta daga gida, ta gaya mata, kana sai waccan ta buga kirji ta ce mata, “Wayyo Allah ! Ai wannan mutum ya batad da ke. Kun bar hanyar Masar tun daga birni."

Uwata ta yi kurum kawai ta rasa abin da za ta fadi. Zuwa can ta ce, “Kaico ! Ni wance yaya zan yi ? Ga shi mun yi tafiya mai nisa, babu damar in koma. Kudin da na fito da su daga gida ma sun kare.”

Waccan ta ce, “In kin ji shawarata kada ki nuna masa kin gane dabararsa, sai ran da Allah ya sa kuka isa Murzuk, sa'an nan ki yi kararsa."

Sun Isa Murzuk

Ado ya dawo kasuwa wajen la'asar, da almuru ta yi sai suka tashi. Suka yi ta tafiya kwana da kwanaki har ran nan Allah ya kai su Murzuk. Su Larabawan da ke cikin ayari kowa ya tafi gidansa, Ado kuma ashe yana da gida a garin, sai ya dauki uwata da kayansa suka tafi can suka sauka. Bayan sun kwana biyu sai Ado ya ce wa uwata, “Kada ki yi tsammani ba zan tafi da ke Ber Kufa ba. Ina so ne in na gama ciko mu bi ta can sa'an nan mu koma gida tare.”

Ya yi ta magana, ita kuwa ba ta ce masa ko ci kanka ba, har ya kare ya yi shiru. Ta bar shi kurum, sai da duk ta ga ya shirya komawa gida. kana ta ce, “Zan kai kararka wajen Alkali.”

Ado ya ce, “To, je ki wurin Alkalin mana, in gani ko ya iya kwace ki daga gare ni !“

Sai Ado ya fita abinsa, bai zame ba sai gidan Alkali, ya ce masa, “Wata baiwa ce na zo da ita daga Kasar Hausa, amma na ga hankalinta ya tashi, in zan koma lalle ba za ta bi ni ba, gama ta ce za ta yi kara ta gare ka."

Alkali ya ce, “To, na ji, Allah ya kawo ta.”

Ado na komawa gida, sai ta fita ta yi kararsa gidan Alkali. Alkali ya tambaye ta abin da ya kawo ta. Ta ce, “Ina karar wani mutum ne wai shi Ado, tun daga Kano ya ce in biyo shi zai kai ni wajen dana, ga shi kuwa mun dade a hanya ban ga alamar zai kai ni ba. Ni kuwa ban san kowa a nan ba wanda zai nuna mini hanya."

Alkali ya tambaye ta, “Wane gari danki ya ke ?”

Ta ce, “A Ber Kufa cikin Kasar Masar.”

Da Alkali ya ji haka, ya gane lalle ba ta da wayo, sai ya ce, “In don wannan ne abu ne mai sauki ! Sai ki zauna a gidana har in sami mai tafiya."

Da yamma ta yi Alkali ya aika aka kira Ado, ya kawo ’yan kudi ya ba shi ya ce, “Shi ke nan, koma gida, magana ta kare. Ka sauka lafiya.”

Uwata tana nan gidan Alkali sai wani mutumin Tarabulus sunansa Ahmad ya gan ta, ya ce wa Alkali yana so ya fanshe ta ya tafi da ita. Suka yi ciniki ya biya Alkali.

Alkali ya kira ta ya ce mata, “Ga shi na sami mutum wanda zai tafi da ke Ber Kufa zan hada ku da shi ya kai ki inda danki ya ke.” Sai ta yi ta murna da farin ciki, ta yi masa godiya.

Kashegari suka tashi suka yi ta tafiya har ran nan Allah ya kai su Tarabulus da magariba. Shi mutumin kuwa bai zame ko ina ba sai gidansa. Da gari ya waye ya kira babbar baiwarsa ya ce mata, “Ga wata ’yar’uwa na samo miki, kome a ke yi ku yi tare.”

Da uwata ta ji haka, ta ce, “A‘a ! Maigida, kai da Alkalin Murzuk ya hado mu ka kai ni wurin dana, sa’an nan ka ce ni baiwarka ce ?"

Ya ce, “Da dai ba haka ba ne, ni sayo ki na yi daga hannun Alkalin Murzuk.”

Sai ta ce, “Haka ne." Ta koma tana cewa, “Ni dai, Wance wahalar duniya ta same ni, saura Allah ya kyauta.”

Ta yi zamanta, ba ta nuna kamar abin ya yi mata ciwo ba, har dai ta ga an saki jiki da ita sarai. Ran nan aka aike ta kasuwa, sai ta zarce gidan Alkali ta yi kara. Alkali ya sa aka kirawo Ahmad. Da ya zo ta mai da jawabi. Shi kuwa ya ce, “Karya ta ke yi, na sayo ta ne a hannun Alkalin Murzuk."

Alkali ya ce, “Shi ke nan, ki koma gidansa ki zauna. Zan yi takarda wurin Alkalin Murzuk, duk abin da ya fadi idan amsa ta komo zan neme ku."

Da suka tashi Alkali ya rubuta takarda ya aika wa Alkalin Murzuk. Ana nan ana nan amsa ta komo, Alkali ya sa aka kiran su, ya ce mata, “Na sami amsa daga Alkalin Murzuk, ya ce karya ki ke yi ya sayar masa da ke ne. Sai ki tafi ki zauna, ki yi ta bauta.”

Ta ce wa Alkali, “Na ji,saura Allah ya isa tsakanimmu.” Ahmad ya yi sallama, ya tashi da kuyangarsa.

Da suka koma gida ya ce mata, “Tun da ya ke kin nuna mini wannan hali, ba zan bar ki a sake ba, zan daure ki har lokacin da kika sake halinki.” Ya sa aka buga mata mari. Dukan aikin gida mafi tsanani, ita ta ke yi, abinci ma ba ya ba ta sai lokaci lokaci. Ita kuma sabo da bakin ciki da zullumi duk ta rame ta fita kamarta, in ta gama aiki sai ta yi zugum tana ta kuka. "

Da ya ga haka a ransa ya ce, “Wannan baiwa ta cika shegantaka, maganinta sai duka.” Kullum kullum sai ya buge ta, amma duk da haka ba ta bar halinta ba. Haka ya yi ta yi mata azaba misalin shekara daya. Amma ita dai duk wuyar da ta sha ba ta dame ta ba, kullum abin da ta ke tunawa a ranta shi ne rashin saduwa da danta, har ta kare ta kasa aiki, sai yawan koke-koke.

Ubangijinta ya rasa abin da zai yi da ita ya ce, “Lalle in na bi ta wannan baiwar banza zan kashe ta in yi hasarar kudina.” Ya kwance ta, amma duk da haka ranta ya ki kwanciya, sai dada lalacewa ta ke yi.

Na Yi Mugun Mafarki

LOKACIN da ina tsakiya jin dadina a Ber Kufa, babu wani abin da ya sha min kai, na manta da kome na kasar Hausa, sai wata rana bayan lisha na tashi na yi alwala, na dauko Alkur’ani ina dubawa kamar al’adata ta kullum, sai barci ya share ni. Ban yi nisa cikin barci nan ba, sai na yi mafarki, ga ni a kan dutse mai tsawo a bakin wani babban kogo. A cikin kogon akwai zakanya da ’yarta. Da ma muna tare da wadansu maharba ne masu farautar zaki. Kafin a jima kuwa da na waiwaya sai na ga babu kowa a kan dutsen, sai ni daya da zakanya da ’yarta. Sai ga ta ta fito daga kogon za ta tafi cikin daji ta yiwo farautar abinci. Bayan da ta tafi kadan, sai na ga ta dawo ta shiga kogon. Da shigarta sai ta juyo a guje, tana raratu da gurnani, ashe ba ta ga ’yarta ba. Ta yi ta zaga dutsen tana kuka, amma ba ta same ta ba. Kai, na yi dai ta ganin abubuwa barkatai. Da na yi kusan farkawa, sai na ga gyatumata a bakin kogon zakanyar tana kiran sunana.

Da ganin wannan sai na firgita, na tashi a dimauce na gigice cikin tunanina. Na yi ta tuna wannan mafarki a cikin raina, na dade ban bayyana wa kowa ba. Sai na kasa daurewa dai na tafi na gaya wa maigidana Abdulkarim. Na ce masa, “Yau raina ya baci. Abin da na fi kawowa cikin zuciyata

dai shi ne uwata tana nemana kuma na ga duk hankalina ya koma cikin kasarmu, amma ban ga yadda zan yi in gan ta ba har abada.”

Sai Abdulkarim ya ce, “Ni ma ina cikin tunanin yadda zan sami ikon komawa Kasar Hausa, domin abin nan da mu ke rainawa ya gawurta, kasar Sudan duk ta lalace, jama’ar Mahdi sun rinjayi Kasar, ban ga alamar Masar za ta sake samun iko a kansu ba. Ga shi kuwa duk kayan da na shirya na sayarwa a can suna nan a ajiye a banza. Amma jiya na sami labari daga wani dan’uwana wanda ya tafi ciniki a Tarabulus cewa ta can ayari su ke bi zuwa kasar Hausa, ita ma babbar hanya ce, tafi wadda muka biyo da kyau. Domin haka abin da na yi shawara, in tafi bakin teku in shiga jirgi zuwa Tarabulus, daga nan in sami ayari zuwa kasar Hausa. To, in Allah ya yarda zan tafi da kai, kuma zan kai ka har garin da gyatumarka ta ke. Amma fa ina da sharadi daya wanda za mu yi. Ina so ka yi mini alkawari cewa in mun tafi za mu dawo tare. In kuwa ka san in mun je kasarku za ka yi mini halin ’yan duniya ne, ka gaya mini tun da wuri in sani. Ina so kuma ka tabbata a cikin ranka, ko ka ce mini in ka je ba za ka dawo ba, shi ke nan, ba zaa matsa maka ba. Domin ka sani na maishe ka dana, kuma kai ne na zuba wa ido."

Na kasa kunne kawai har Abdulkarim ya kare magana tasa, sa’an nan na ce masa, “Yau a duniyan nan na sani ba ni da wani uba sai kai, a hannunka na girma, kai ka sa ni cikin mutane to, ina ka ga hanyar da zan guje ka?Ai yanzu ka sani koda ya ke dai wani akan yi masa rana shi kuwa ya kan yi dare ai ba irina ba ne. In na yi maka haka ai Allah ya tambaye ni."

Muka zauna muka yi ta tadi da Abdulkarim har kusan azahar, sa'an nan ya ce in tafi gida, domin almajiraina sun fara taruwa. Da na tafi na sami masu daukar karatu sun taru da yawa a gindin itaciyar kofar gidana, kowa ya bude littafinsa yana yin bita. Sai na shiga gida na yi wanka, sa‘an nan na fito na ba su karatu. Bayan na gama ba da karatu sai muka tashi, kowa ya yi alwala, na wuce gaba muka yi salla. Da muka idar sai na ba su labari cewa a cikin wannan wata da mu ke Abdulkarim ya ce za mu tafi in dubu gida cikin yardar Allah. Da na fadi wannan ban ga sun yi farin ciki ba. har na tambaye su dalili. Suka ce wai abin da su ke tsoro ko in na tafi gida ba zan dawo ba. Na shaida musu wannan ba haka ba ko kadan.

Cikin watan azumin tsofaffi da kwana tara muka kare shiri muka tashi. Muka shiga jirgi, muka bi igiyar kogi har muka kai Birnin Masar. Daga nan sai lskandariya, inda muka sami babban jirgi. 'Yan kwanaki kadan sai ga mu a Tarabulus.

Da muka sauka daga jirgi sai Abdulkarim ya tambayi wani mutum ya ce yana so ya fada masa ko akwai wani a garin wanda ya saba ta'ammali da kasar Hausa.

Ya ce masa, “A garin nan dai babu wani mashahuri sai Ahmad.“ Ya tafi da mu gidansa. Ahmad ya yi mana maraba, ya saukad da mu ya yi mana karimci mai yawa.

Bayan mun huta ran nan sai Abdulkarim ya zo suna tadi yana tambayarsa labarin hanya, Ahmad ya gaya masa iyakar abin da ya sani. Abdulkarim ya ce, “In Allah ya kai mu gobe zan tashi."

Sa'an nan Ahmad ya ce masa, “Ina da wata baiwa mutumiyar Hausa, wadda na sayo ta daga Murzuk bara, amma ta cika mugun hali, tun ran da na sayo ta ba ta yi mini wani amfani ba sai dada lalacewa ta ke yi sabo da tunanin kasarsu, in ba na rabu da ita yanzu ba sai in yi hasarar kudina. Kai kuwa da ya ke cinikinka ne, ga shi kuma kana jin harshensu, watakila ka san maganinta, ni dai in rabu da ita."

Abdulkarim ya ce, “Ina ta ke ?"

Ahmad ya shiga ya yi kiranta ta fito. Da ta fito sai Abdulkarim ya ce, "Sannunki !"

Da ta ji ya yi mata magana da harshenta, sai ta fadi gabansa, tana kuka. Ya tambaye ta, “Me ya same ki ? Ke kuwa mutumiyar wane gari ce ?"

Ta ce, “Ni mutumiyar Fatika ce, mijina yana can a wani gari ana ce masa Makarfi, can na bar shi."

Ya ce “Yaya aka yi kika zo nan ?"

Sai ta shiga ba shi labarin yadda ta fito garin neman danta, da yadda aka yi mata wayo aka sayad da ita, har zuwanta wannan gida. Da ta gama ya ce mata, “Yanzu me ki ke so ?”

Sai ta ce, “Ai ba abin da na ke so kamar in cika abin da ya fito da ni daga gida, in samu in ga dana sa'an nan in na so in mutu."

Da ya ji haka sai ya yi mamaki karfin halinta ya ce, “Kin san sunan garin da danki ya ke ?"

Ta ce, “I, domin an gaya mini wani mutum ne ya tafi da shi garinsu a kasar Masar sunan garin kuwa Ber Kufa."

Ya ce, “Ber Kufa ! Ina sunan maigidansa ?"

Ta ce, “Wai sunansa Abdulkarim."

Ya ce, “Abdulkarim ! Ina sunan yaron ?"

Ta ce, “Umar.”

Da ya ji haka, ya ce, “Allahu Akbar ! Allah mai yin yadda ya so ! Ki yi murna, Allah ya dube ki, yau wahalarki ta kare."

Sai ya juya wajen Ahmad ya ce masa “Nawa zan ba ka in fanshe ta ?"

Ya ce, “Kome ka ba ni, shi ke nan."

Ya tafi ya kawo kudi ya ba shi. Sa’an nan ya kira ni, ya ce mata, “Ga wanda ki ke nema. Kuma ni ne Abdulkarim."

Mahaifiyata Ta Gan Ni

Sai ta dube ni ta ce, “Umar ! Kai ne ?" Sai ta fashe da kuka. Ni dai ina tsaye ina mamaki, sai na ji jikina ya yi sanyi. Na tambayi Abdulkarim, “Wace ce wannan ? Ina dalilin da ta ke kuka ?"

Sai uwata ta amsa ta ce, “Ni ce mahaifiyarka, shekarun nan da yawa ina nemanka, sai yau Allah ya hada mu.” Ta yi wuf ta rungume ni, ni dai na kasa magana.

Sai Abdulkarim ya ce mu tafi masauki. Da muka tafi hankalinta ya komo, ta yi ta ba ni labarin abin da ya same ta duka. Ni kuma na gaya mata nawa.

Sa'an nan na ce, “Yanzu dai sai na kai ki gida, in Allah ya yarda."

Sai ta ce, “Kayya ! Na rabke. Na sani ba zan koma gida ba, amma tun dai da na gan ka ya ishe ni. Kai dai Allah ya kai ka gida, ka ga sauran danginka."

Na ce, “Kada ki ce haka, Allah ya Sawwaka."

Ashe karfinta ya rigaya ya kare, sabo da wahalar da ta sha, ga kuma murnar ganina ta yi mata yawa. Daga nan ba ta kara tashi ba. Ashe Allah ne ya sa muna da rabon ganawa. Bayan kwana kadan sai ta rasu. Muka yi mata sutura. Da ta yi bakwai muka mika. Ni dai tafe na ke kawai, amma zuciyata tana cike da tunanin abin da ya auku a gare ni. Kwanci tashi, ba abin da ya same mu a hanya har muka kai Murzuk.

Da muka sauka a Murzuk, ba mu sami ayari masu wucewa ba, sai muka zauna nan watanni, sa'an nan muka sami wadansu muka wuce.

Mun Ci Gaba Da Tafiya

DA muka tashi daga Murzuk muka yi ta tafiya kamar wata uku, har Allah ya kai mu wani dan kauye wai shi Muhtad. Da saukarmu sai muka fantsamu muna tambayar labarin hanyar da za mu bi. Kowa muka tambaya kuwa sai mu ji wai hanya ta baci, babu abin da a ke yi sai fashi da yakoki tsakanin kabilu. Da muka ji haka sai manyan tafiyarmu suka taru domin su yi shawara a kan abin da za a yi. A wurin fa, sai bakinsu ya saba. Wadansu suka ce a koma, wadansu suka ce a ci gaba. Kai, a cikin shawarwarin nan ne na ga inda a ke son dukiya. Dukansu kowa sai duban ribar da zai ci kawai ya ke.

Da wadanda suka ce a ci gaba suka rinjaya sai kowa kuma ya yarda, aka yi ta shiri domin mun yi niyyar tashin dare ne.

Da gama cin abincimmu sai aka buga kuge, muka tashi. Muka sake hanya sabo da tsoron mayaka, muka ratse cikin hamada. Wannan sakin hanya fa ya zama babbar hasara a gare mu. Tun da muka tashi daga Muhtad muna tafiya a cikin dare ba mu gamu da kowa ba, ba mu kuwa ji motsin kome ba, har gari ya waye mana a kusa da wadansu manyan tuddan yashi wadanda iska ta tara. Da muka kai wurinsu nan rana ta bullo sai madugu ya ce a huta har rana ta yi sanyi kana a tashi. Muka sauka, kowa ya debe wa rakuminsa sirdi. Muka yi kwance bayan da muka sha ruwa muka ci abincimmu. Muka zauna a wurin, masu yawo suka tafi, masu barci suka yi, masu karatun Alkur'ani suna yi, masu tadin duniya kuma suna yi. Kowa dai daga cikimmu yana aikata abin da ya ke bukata har rana ta take tsaka cur.

Yayin da kowa yana cikin hidimarsa, an sake sarai, sai muka ji kuwwa daga wajen 'yan'uwammu da suka tafi yawo, muka hango su a guje rididid kamar garken Uda. Mu duba haka wajen gabas sai muka ga wani abu can baki kirin kamar hadari, daga kasa ya tokare da samaniya, ya nufo inda mu ke. Ni kam ban san ko mene ne ba, amma sauran mutane da mu ke tare da su sai na ga kowa

ya fara tara kayansa yana kuka. Ni kuwa sai na tsaya kawai ina ta kallo, ban san abin da a ke yi ba. Zuwa can in daga kai dai, sai na ga abin nan a gabana kamar hadari. Ashe ba hadari ba ne. Iska ce kawai ta girma ta zama haka. A cikin iskar kuwa ba kome sai yashi. Yayin da iskar ta kawo wajen da mu ke nan da nan sai na ga duk wurin ya hargitse, ba ni iya ganin kome balle in san inda yan ’uwana su ke. Sai na dame, na rasa abin da na ke ciki.

Ni Kadai Na Tsira Bayan Hadari

Kada dai in kai ka da nisa, iskar ba ta tashi yin sauki ba sai bayan lokaci mai tsawo, kana ta d'an kwanta. Da idona ya waye na duba cikin sarari sai na ga babu kowa sai ni daya. Kuma tuddan nan na yashi da muka sauka gindinsu ban ga alamar ko daya ba. Sai tsoro ya kama ni, a raina na ce lalle halakata ta zo. Sai kuma na tuna da maigidana da sauran jama'ar da mu ke tare dasu, gama zuciyata ta saka mini cewa lalle yashi ne ya rufe su duka. Na yi ta zagawa ina kiran Abdulkarim, ban ji amsa ba ko motsi, har na gaji. Sai na zauna, na fashe da kuka; lna cikin haka har gari ya rufa. Nan na kwana a sararin Allah, ko barci na kasa yi.

Da gari ya waye na tashi na sake zazzagawa ko na ga wani mai rai. Ban ga ko alama ba. Na yi ta yawo kawai ban san inda na ke nufa ba. Kwana uku ina haka, dan ruwan da na ke da shi cikin butata ya kare. Kishirwa ta kama ni, ga zafin rana, wurin fakewa ma babu. Sai na kasa ko tsayawa balle tafiya. Na yi kwance kawai, ina jiran mutuwa.

Rana ta hudu wajen la’asar ina kwance sai na ji kuka kamar na rakumi, gabana ya fadi, na daga kai, sai na hango wani rakumi daga nesa da labtu ya nufo inda na ke. Na ce, “Hakika Allah shi ne mai iko !" Ina zuba ido kawai har ya iso gare ni, yana sansane-sansane. Ya tsaya, na dube shi, ashe rakumina ne, sai na ga ya durkusa a gabana, na ja jiki na kai gare shi, na rarumi salkar ruwa, na sha. Hankalina ya komo, na debo dan abinci na ci, na yi godiya ga Allah. Na kwana a nan tare da rakumi.

Da gari ya waye na ji karfi, na kintsa kaya na hau, rakumi ya mike a tsaye. Ina zullumin ta inda zan bi, sai na ga rakumina ya kama wata hanya da kansa. Ni kuma da na ga haka ban yi wani zumudi ba sai na bar shi ya yi ta tafiya, har ran nan sai na fara hangen wadansu bishiyoyi na

dabinai daga nesa. Da muka iso wajen da itatuwan nan su ke sai na ga babban gari ne. Rakumina ya yi ta tafiya har ya kawo ni bakin wata rijiya, ya ja ya tsaya. Na sauka daga bayansa na debo ruwa na ba shi, ni kuma na je gindin wata itaciya, na zauna a kusa da wadansu ayari. Na same, su suna tadi, na ji suna cewa wai rana ya ta yau war haka, in Allah ya so, suna Birnin Kuka cikin kasar Barno. Suna ta tadinsu, ni kuma ina ta murna a cikin zuciyata na sami masu zuwa kasarmu.

Muna zaune a gindin wannan bishiya muna tsakiyar tadi ke nan sai muka ji an yi ihu daga cikin gari. Nan da nan sai muka ga mutane suna ta fitowa a guje. Ba a dai jima ba sai muka ga duk garin ya fashe, kuma muka hango wuta ta kama gida. Mu muna zaune, ba mu san abin da ya auku ba, sai dai hankalimmu ya ba mu cewa lalle ba lafiya. Duka sai muka tashi, kowa ya yi shiri. Muka hau rakumammu, muka yi tsaye a kan kayammu.

Ba mu jima ba da gama shiri sai muka ga rundunar wadansu mutane da bindigogi. Da ganinsu muka watse, kowa ya kama hanyar da ya ga za ta fisshe shi. Muka yi ta gudu. Yawancimmu da suka tashi gudu sai suka nufi ta inda suka fito, watau cikin hamada. Ni kuwa da dai na ruga a guje bisa kan rakumina sai na nufi wajen da masu bindigogin nan su ke. Na zo na wuce su a guje. Na yi ta gudu har na kawo zuwa wani gari babba mai yawan itatuwan kuka. Na zo wani gida na sauka daga kan rakumina, duk hankalina ya fita daga jikina.

Mai gidan ya fito, ya ce mini, “Yanzu daga ina ka ke ?"

"Na ce masa, “Daga wani gari ne wadansu 'yan yaki suka koro mu."

Shi kuwa ya ce, “Lalle wadansu daga cikin mutanen Rabe ne wadanda suka barko bayan da Faransai suka kama shi suka kashe."

Yadda Na Iso Rauta

A garin nan fa ban sami tashi ba saboda rashin lafiyar rakumina. Da na kwana shida a wurin sai ya mutu. Bayan mutuwarsa da kwana biyu sai na tashi zuwa kasarmu a kasa. Kwanci tashi, har Allah ya kawo ni wannan gari naku Rauta. A nan na ji labarin Makau ya mutu. Ba ni da sauran

dangi wadanda zan tafi in dubo, sai na yi zamana a nan ina karantarwa. Ka ji dalilin zuwana kasarku ke nan.

Alhamdu lillahi Allah kai ne abin godiya. Ina rokon Ubangiji ya gafarce mu bisa kan abin da muka aikata da kuma abin da za mu aikata zuwa gaba. Allah Ubangiji ka kore mana huznu da hassadar magabta, ka kubutad da mu daga sharrin duniya da na lahira, amin.

## SHIRYAWA

(c) 2017 Bukar Mada

bukarmada@yahoo.com

WhatsApp: +2348021218337

Facebook: @bukarmada

Twitter: @bukarmada

Instagram: @bukarmada

Za a kuma iya samun wasu littafan a shafin Taskar Bukar Mada:

http://bukarmada.blogspot.com